Dole nai kuka Dan Ina tausaya Miki kun shaku soyayyarku abar Sha awace da burgewa duk yadda muka Kai da shakuwa Wanda yafi mu sansa ya karbi abunsa ki tashi ki shirya na dauka umma tana Nan zamu tafi tare gidan Jana'iza babana yai gaba Inna tana gida tace nazo na kiraku haka suka shirya suka tafi da innar ta hawaye kawai take tana salati a zuciyarta tana rokon Allah ya Bata juriya da dangana na rashin masoyinta zuciyarta sai zafi take

Lawan Yana fita be zame ko inaba sai gidansu Laila yana zuwa ya aika a kirata tana fitowa ya kalleta ta cika Tai dam kamar zata fashe shiga mu tafi kawai yace ta shiga motar hotel din da suka Saba zuwa suka nufa suna zuwa hotel din ya Karbi key dinsa Dan shi permanent ne suka shiga Nan ya Fara shafata Yana Bata hakuri ganin haka ta Fara jaraba rashin mutunci harda zagin ummi har kiransa take da Dan iska Yana Jin tazagi ummi ya Mike ya zabga Mata Mari ya Fara dukanta sai dayai Mata lilis sannan ya nemi gu ya kwanta Allah ya Isa bazan yafeba Dan iska tsinanne be kulata ba Dan ze iya kasheta idan ya Mike

Haka ta zauna taci kukanta shi Kuma yaci baccinsa sai gab da magriba ya farka yaga itama baccin ya dauke ta yai murmushi Laila Ina sanki Amma hakan baze Hana idan kikai mun lefi na zanekiba Dan hukuncin ne haka idan ummi ta tabaki zan rama miki itama idan kin tabata zan rama Mata ya dinga shafata Dan ba lefi tanada da dadi duk da bashi ya Fara bulataba Amma bataji jiki sosai ba ta farka tana ture shi Ina yasan takan mace Nan ya gama gigita Mata tunani yadinga sarrafata San ransa kafin kace meye wannan ta bada Kai bori yahau

Sai da suka nutsu suka Gama komai gaskiya Laila adaura Mana aure haka Koda Baki tare ba daga baya Kya tare kafin na gyara Miki saman gidana auren mashayi kenan duk wannan dukan Tama manta da shi eh haka za ai saboda Yana side ta tas Kuma ba abunda yafi dadi irin mijinki

ya gama lugwiy gwiy Taki kafin Yafara harka zanwa daddy na magana ni kaina nagaji nafiso a daura Mana aure nima na huta shikenan sweety Nan ya jawota suka Kara one round Allah ya shirya ameen lokacin da suka Gama dare yayi ya maidata gida ko tsoro Babu a fuskarta haka ta shiga gidan

Bayan sun shiga gida arfan ya fito yayi kyau kamar ka sace shi ka gudu ya Sanya manyan Kaya wandon pencil shaddar sai daukar ido take kamar Wanda zashi office da gaske Nan ko basaja yai dankar ta gane tunda baze yiwu kullum ya dinga cin zanzaro ba Yana fita Yana zuwa club Shiba me zuwa aiki ba haka kawai har sun Fara yi Masa dariya yammatan sa wow dear bara naima pics Nan ta Fara daukansa hoto sai dariya suke dukansu Banda Maryam dataji ta tsane shi tsana me Muni wannan wace irin rayuwace wace irin zuciyace da yayar tata

Ita Sam bazata dau wannan iskancin ba akan me namiji kullum yace ya tafi aiki to Wai aikin me ma yakeyi ne yau zata tambayi yayarta ransu Kal ko kunya suka Gama kiss din su ta raka shi har mota yaja ya tafi nafeesat ta dawo cike da farinciki Maryam ta Gama kuluwa Banda wawiya yaushe Zaki raka mijinki Dan ze tafi yawon iskan cinsa wannan takai ci dayawa yake

Sister nafeesat ta tabota ta juyo lafiya anty Naga kin yafi tunani lafiya muje mu kwanta ko eh Amma na tambayeki Mana anty Wai meye aikin Yaya arfan ne Naga kullum sai ya fita da daddare sunan aiki Kuma Naga Shiba wani aikin force yake ba bare nace anty Ina mamaki shiyasa na tambayeki shekewa tayi da dariya

Woooo autar Mama rigima arfan Dan gidan alhaji kamalu shakara ne duk wani company da Kika ga ansa shakara investment Nigeria limited to na babansa ne Dan dai bamu taba wannan hirar dake ba tunda sai gab da bikinmu kukai candy Kinga boarding kike shiyasa Amma kowa yasani a gidanmu shakara investment anty fa kikace wannan kudi haka

*Bari na dakata sai min hadu a next page sai naji comment dinku naga dayawa wasu sun gyara suna comment nagode sosai dan Allah fans ku Kara hakuri banajin dadine kwana biyu*

*Nice Taku a kullum a Koda yaushe nake muku fatan alkhairi*

*Feedyn bash*
[10/3, 4:46 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *👳DAN ISKAN NAMIJI👳*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏼
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DASUNAN ALLAH ME RAHMA ME JIN KAI GODIYA TA TABBATA GA ALLAH UBANGIJI INA FATAN ALLAH YA ALBARKACI ARNAN DAJI FANS DA KAINUWA FANS JIN DADIN COMMENT DINKU AGARENI*

*_😍😍😍😍😍😍😍😍😍WANNAN PAGE DIN NAKINE KANWATA TA KAINA SADAUKARWA AGREKI KIYI YADDA KIKESO DASHI NEESHAR JAY MY SWEET KANWA PAGE DIN KINE😜😜😜😜_*
```

13-14

Gaskiya aunty kiyi bincike shakara investment ba abunda basa siyarwa Kama da company travel agent mall ba abinda basu da shi har suya sport Amma anty gaba daya 12 suke tashi masu yinma aikin dare kenan masu Zama a super market da mall da suya sport Amma shi Yaya arfan shine manager a kamfanonin indai shine dansa danaji Ana fada a gari meya hada shi da aikin darene harda yake kaiwa 2 3 a waje want time din ma sai karfe hudu yake shigowa gaskiya anty kiyi tunani

Dariya ta sheke da ita kedai bakya rabo da fitina kanwata ke duk ya akai kikasan shakara family haka Ana labarin su a school dinmune sunyi fice a kafatanin duniya gaba daya Kamal shakara waye besan wannan sunan ba kanwata kwantar da hankalinki dad da mom mutanen kirki ne basu da matsala ga temako kowa yasani a kafatanin garin Nan anaji dasu Dan haka nasan da cewa mijina mutumin arzikine bashi da wata matsala a rayuwarsa shima me temakone to anty muje mu kwanta

Suka mike dama kowa da dakinsa suka wuce nafeesat ta sheka wanka da kwalliya tasa wata guntuwar gown iya cinya ta tafi sama dakinsa ta kwanta itako Maryam Banda tunani ba abunda take dama wannan Dan iskan datakeji Ana fada a gari Dan gidan Kamal shakara arfan dama shine arfan mijin yayarta mikewa Tai Tai nifilfili sannan ta kwanta bacci me nauyi ya dauketa cike da mafarkai barka Tai Wanda ta rasa gane kansu sai juyi take kamar arfan mijintane abun ya tsaya Mata arai tana mugun tausayawa yayarta haka taita juyi Amma baccin ta yai nauyi

Arfan na fita be zame ko inaba sai mozida club Yana shiga aka Fara ihu shakara shakara club ne Wanda ya amsa sunansa club na ta tattun Yan iskane wayanda suka amsa sunansu Yan iska a cikin sabon gari yake ba wani Dan sanda dayake kamashi sun San shi sunsan waye shi sai babban yaro shege uban shegu Dan iska uban Yan iska shagalalle uban shagalallu cike da murna suka dinga yo kansa Bata su yakeba beb dinsa yake nema me suna beauty chan ya hangota jikin wani Nan wani bala'in kinshi ya taso Masa bakinsa har wani daci yake

A fusace yaje wajenta ya wanka Mata Mari ya fusgota ta fada kirjinsa sharaf yaji jikinta zafi zau

beb lafiya meya sameki gayan jikinsa har rawa yake yaro da kudi wallahi ganin ta nai tana tangadi shine na rungumeta ba wani Abu nai mataba ko kallonsa beba ya dauketa sai dakinsa dake hotel din jikin club din Nan yadinga lallabata Ashe tsabar buguwace tadinga kwara amai me wari ransa yai bala'in baci dama haka warin giya yake betaba saniba gashi a jikinsa tayi shi saida Tai me isarta sannan bacci me nauyi ya dauketa takaici ya isheshi ko club din be komaba ya kalleta Dan karta gudu danse ya hukuntata

Yana sauka yaga wata zee ashana  Nan tadinga dirka Masa wata giya Don ga karfi ga tsada yadinga  Sha saboda bacin ransa ya tafi sai da yai tatil yaja motarsa sai gida anci sa a ya kashe motar yau be tashi kowaba Banda megadi daya dinga zabgawa horn Yana zuwa Kai tsaye dakin da Maryam take ciki ya nufa ya cire kayan jikinsa Yana ta tsaki gashi a make yake daga idon daze yaga.....

Sunje har ankawo gawar na hadata anata karatu Yasin ce da addu'oi dai haka akadinga yi Masa sai da aka Gama yi Masa wanka Sam maimuna tace bazata iya ganinsaba Dan anhana Mata ma ganinsa duk wadda taganshi firgicewa take Haka aka dauke shi aka kaishi makwancinsa na gaskiya suka bishi da addu'a nauwara tace zata koma gidan saboda zata dafo abincin sadaka yamma tayi kibarshi gobe kyayi inji maimuna sai dare suka koma gida gaskiya nauwara ta tsorata taci kuka ta tausayawa kawarta

Aranta tayi alkawarin bar Mata alhaji ghali ita Allah ya Bata wani Amma Ina tana komawa gida zance ya sauya tana shiga gida ta tarar umman tata ta dawo ta fada jikinta tanata kuka tana Bata labari har aka kaishi jinine ke zuba eh naji Allah ya temakeni kinsan ban Dade da wowaba I na shigowa mukai kicibis da babanki yai min gaisuwa nai Jim sai yace kobada gidan gaisuwar saurayin maimuna kukeba muma yanzu muka dawo Ina nauwara suna tare da maimuna yanzu zasu taho Allah ya temakeni beja da nisaba bare ya kamani

Ashe haka Abu ya faru Allah ya Bata wani madadinsa umma ai yabata Dan wallahi nabar Mata alhaji ghalinta zanbi zabin da baba yaimun Allah ya basu zaman lafiya Ni Kuma yasa haka shiyafimun alkhairi gaba dayanmu nida ita kan bura uba nizakiwa bakin ciki nizaki rainawa hankali to ubankima yayi kadan bana magana biyu

Yadda Kika kawo shi da farko harna barnatar da kudi Dan aimana aiki akansa to wallahi

tazauna Baki Isa kice Baki sansa ba Dole ki aureshi Dan nasan duk inda yake yanzu aiki ya Isa gareshi baze wuce gobe ba zezo gareki Dan Haka ki nutsu kisan mezakice Masa nagaya Miki wallahi gidansu maimuna zan Kai shi wallahi Dana tsine Miki albarka Dan ubanki danace ba nono na Kika shaba

Ke wallahi danace Sanjamun ke akai ran suna tunda ba'a asibiti na haifeki ba Dan Haka wallahi aure ba fashi ido ta zaro cike da tsoro Allah ya sani dake ita taga gawar Taji tsoron Allah ya shigeta yanzu taji tsoron karta cutar da maimuna ta mutu itama Amma Ina ummanta data zaunar da ita a Daren tadinga yimata huduba tahu Kai tazauna dabas yadda tadinga haska Mata irin yadda zatai mulki a gidan tunda Bata da kishiya zata zaga duk kasar data ga dama a duniya

Washe gari Tai abincin sadaka me Rai da motsi itada ummanta harda nama aka Kai sun tarar dasu maimuna achan dawuri suka dawo tsafi gaskiyar me shi da magariba sai ga alhaji ghali da tambaya danbe gane kwatance ba dake lokone aka kaishi har kofar gidan cike da farinciki aka aika tazo ta Nan ta hau bare bare

*ANAN ZAN DAKATA SAINAJI COMMENT DINKU AKAN DAN ISKAN NAMIJI YADDA DA FARKO KUKE SAN SA KUKA DAMENI NAFARA TYPING AMMA SAM BANA GANIN COMMENT KAMAR HAKA NAGODE MASOYANA NICE YAKU A ME NISHADANTAR DAKU A KULLUM A KODA YAUSHE*

*FEEDYN BASH*
[10/3, 4:46 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *👨🏻‍🔬DAN ISKAN NAMIJI👨🏻‍🔬*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Assalamu alaikum fans kuyi hakuri dani ba kullum zaku dings samun typing  ba saboda wasu dalilai ina bukatar addu'arku  kawai fans duk me kaunata yasani a addu'arsa allah ya yayemun abunda ke damuna yabiya mun bukatata nagode sosai da kulawarku agareni da dumbin alkhairinku agareni musamman masu turon da kati nagode allah ya bar kauna inajin dadin yadda kukemun addu'a da nuna kulawa a gareni nice taku princess feedy cele💃💃💃🥰🥰🥰*

*Wannan page dinsadaukarwane agareki aisha idris abdullahi inajin dadin yadda kike mun comment  nagode sosai  sis allah yabad kauna wannan page din nakine kiyi yadda kikeso dashi inkiso kihana kowama karantawa🤣🤣🤣🤣*

15-16

Idanuwansa ne suka sauka kan wasu luntsuma luntsuman nonuwa ga ta baje akan gado gashinta ya watsu saman pillow jikin nan luf luf fresh tashin hankali besan sanda ya karasa cike da maye ya fada kanta ba ihu ta zindima ya toshe mata baki Yana girgiza mata Kai ya matseta gam a kirjinsa be mata komai ba rungumeta kawai tai bacci yai awon gaba dashi kuka take kasa kasa tana tsoron ta motsa yai mata wani abun a haka suka kwana

Kiran sallar asuba a kunnensa da hanzari ya farka yaga itama ta wani sakalo shi bacci  suke hankali kwance abunma dariya ya so bashi yadda ta wani makalkaleshi ta turo dan bakin ta fuskarta tai jajir shedar tace kuka kare mata kallo kawai yake I love you ya furta ya Zare jikinsa a hankali yadda bazata farka ba dake shi namijine ya nufi samansa yatarar nafeesat nata sharar bacci tausayinta yadan tsirga masa amma shi Sam Ashe ba Santa yake ba yanzu yaji real love daga wajen kanwarta Ashe ita sha'awarta yake tunda ya biya bukatarsa Sam yaji wannan abun dayake ji game da ita ya tafi yaso ajiye iskanci daga aurensa amma baze iyaba
```

yasaba

Bandaki ya shiga yai wanka sannan yai sallah sai ya tashi nafeesat taje tai sallah my life yaushe ka dawo nadade da dawowa dear a gida na kwana jeki sallah kema kizo mu kwanta ta mike ta tafi toilet mikewa yai ya salallaba ya koma kasa ya tarar da ita tagyara kwanciyarta santala santalan cinyoyinta duk a waje tsayawa yai ya shagala da kallonta chan ta farka ta duba ko ina bataga mutum ba ta fashe da kuka kenan mafarki nake wallahi ba mafarki nake ba shine ko aljanune tunda banji karar motarsaba baba kacuceni ina shirin zama zautacciyya ka hadani zama da dan iskan namiji wanda ze IYA lalatamun rayuwata

Ransa ya baci shitake Kira dan iska wallahi zata san ta kirashi dan iska juyawa yayi ya koma saman sukai kicibus da nafeesat my life nafito naga baka nan har na idar da sallah shiru eh naje nabada wani sako ne ok shikenan mukoma miyi bacci dazan taya maryam girkine ki kyaleta ta dafa ita Kadai muje suka wuce sama suka raya sunna sannan suka kwanta bacci sai sha daya suka farka

Laila ce gaban babanta tana fada masa kudirinsu shibaze Iya wannan jarabar ba tun kan ta dakko masa jaraba take ya yarda yace ta turo lawan din zasi magana tana shiga gida ta Kira lawan tagaya masa komai yaji Dadi shima da daddare sai gashi yaje suka tsaida magana sati biyu masu zuwa Za'a daura auren yaje ya turo waliyyansa manyan unguwa yanema wayanda sukai zaman mutunci da iyayensa ya gaya musu su kuma ganin sunna ze raya suka amince ko allah zesa ya shiryu ta haka

Rana bata karya sai dai uwar diya taji kunya lawan ya tanadi komai nasa na lefe ankai masa Ana I gobe daurin aure abokansa suka hada musu dinner a durbar hotel  angayyaci cikakkun tantiran YAN iska su dan asharalle angayyaci makada na shargalle suka tafi dinner din ango da amaryarsa sunyi kyau itama ga kawayenta masu budadden ido irinta anbaje haja ta iskanci a wannan rana anyi iskanci maza haka suka dinga sasikar mata

Dama a hotel suke nan lawan ya hango wata tayi masa ba karya garda gar yace da amarya ta tafi gida tazo akaita tace to suka fito yasa akaita gida ya koma suka sasanta da wacchan tunda harkace ta iskanci Ashe  amarya bakam tai bata tafi ba tasa aka maidota ta tambayi abokansa a wane room yake kowa tsoro yakeji meze faru idan suka nuna ta Haukace musu dole suka kaita tadinga kwankwasawa da karfi yarinyar tacire komai sai bra da pant shike gogan kawai rigar ya

cire ko singilet be cireba mtswww waye wai ba amsa a fusace yazo ya bude kofar waze gani

Laila ce duk da yadan girgiza amma sai ya tuna shifa dan iskane mace bata raina masa hankali dan haka ya daure fuska me kika dawoyi bance ki tafi gidaba bazan tafi ba munafiki algungumi ba inda zanje ta fakaice shi ta ingijeshi ta shige da gudu tai kan yarinyar kamar wata mahaukaciyar kura ta chafketa tadinga duka zan nuna miki nafiki iskanci rike ta yayi yanaso ya kwace ta daga jikin waccen amma ina taki saida tayi mata kacha kacha da bra duk ta yakushe mata nono fuska tasha yakushi ransa ya baci ganin taki bari ya zabga mata mari

Yajata waje ya kullo dakin da gudu yarinyar ta murza key tanata doka kofar kamar zata balla ran lawan yaje makura a baci yajata kamar kayan wanki a kasa a harabar wajen kowa ya fito ya dinga dukanta ya cire belt dinsa yadinga kwallo da ita yajata waje ya hada kanta da bango ya zari wata igiya ya daure ta anata bashi hakuri yaki sauraron kowa kowa yasan halinsa dan iskane na abuga a jarida kowa baya shiga harkarsa Sunsan ba mutunci ne dashiba beki ya wulakanta duk wanda yasoba kowaye ya daure ta a jikin salansar motar ya bude ya shiga kowa ihu yasaka a wajen

*Muhadu a next page bakwamun comment  dayawa shiyasa bana typing dayawa gaskiya more comment  more typing nice taku a koda yaushe*

*feedyn bash*
[10/3, 4:46 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *💆🏻‍♂️DAN ISKAN NAMIJI💆🏻‍♂️*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DA SUNAN ALLAH ME RAHMA ME JIN KAI GODIYA TA TABBATA GA ALLAH UBANGIJI*

*ASSALAMUALAIKUM FAN ALLAH FANS KUYI HAKURI KUNJINI SHIRU KWANA BIYU BANMUKU POSTING DIN DAN ISKAN NAMIJI BA AMMA KUYI HAKURI UZURIRRIKA SUKAI MUN YAWA INSHA ALLAH IDAN KOMAI YAI NORMAL ZAKU DINGA JINA NICE TAKU FEEDYN BASH INA GAISUWA MASOYANA INA GANIN SAKONNINKU WAYANDA BANWA REPLY BA SUYI HAKURI ABUBUWA SUNMUN YAWA PRINCESS FEEDY CELE KE GAISUWA💃💃💃💃💃*

17-18

Ya Fara Jan motar wani  abokinsa ya hango wani karfe da gudu yaje ya dauke shi ya saiti gaban motar yasha gabansa wallahi kanaja saina rotsa gaban motar shege Dan iska Wanda besan mutuncin kansaba wakaga Yana Haka amaryar daza adaura muku aure gobe kake jibga akan karuwa lawan Yana mota yaki fitowa wani irin ajiyar zuciya yake saukewa gashi fari Nan da Nan fusakarsa Tai jajur itako karuwar da kyar aka fito da ita daga dakin a tsorace take ganin yadda Laila ke kwance cikin jini fuska a kumbure sintim gata kwance daure da igiya

Ga dukkan alamu ma ta Suma mutane nata nuna akanta ya daki amaryar sa lallai Yana yinta sai lawan babban Dan iska tanajin wayannan maganganu ranta kal ta karasa bakin motar ta bude Masa ya zuba Mata ido ta kamo hannunsa ya biyota kamar rakumi da akala Nan wasu sukai sauri suka kwance Laila da numfashin ta baya fita beb din ta sakalo hannunsa sun Fara tafiya ta cire ta juyo inda Laila take ta tsirta Mata yawu Dan ubanki kadan Kika gani saini me
```

lawan nasan ba abunda baze iyaba akaina hakan bemata ba tana kallonta kwance cikin jini Amma tafara dukanta mutane na riketa tana dukanta da kafa lawan na juyowa yaga abunda ke faruwa a fusace yayo kanta

Ya fisgeta da karfi yajata suka wuce dakinsu hankali kwance suka Fara aikata badala yarinyar tayi Masa yadda yakeso zasu Dan Dade tare Dan tanada juriya sabanin Laila ragwanta Haka suka kwana suna bau daya sai asuba sanda kowa ke ibada sannan suka kwanta bacci rungume da juna wannan ranar ita takama ranar daurin aurensa da la laila hankali kwance yake baccinsa Dan yasan Laila namasa San da Dole ta yarda a daura tunda ta Zama guzuma aure takeso kodawama ta samu

Bayan sun shige ciki aka zubawa Laila ruwan sanyi tadan farfado Amma ko yatsanta Bata iya dagawa Haka abokansa dayazame musu Dole dansu lalacewar tasu Bata Kai Nan ba wasu daga ciki suna mutunta matansu suka sata a mota suka kaita gida suka Kira babanta ya fito ransa a bace Amma ganin Laila cikin jini hankalinsa ya tashi dannan lafiya meya same ta haka jikinsa yai sanyi baze iya dubansa yace Masa abokinsa ne yai Mata wannan dukan kamar wata dabba cikin kinkina accident suka samu ne jikinsa rawa yafara

Ya Salam ashsha garin Yaya Ina shi lawan din ai Yana chan a sume tunda yaji abunda ya faru baban ya riketa da sauri muje asibiti suka juya akalar motar suka nufi private hospital dakyar suka amsheta shima Dan da babantane Amma daga ganin wnn b accident bane dukane cewar doctor duka ya zaro ido suko tuni sun samfe waye ze Mata wannan dukan yanata mamaki yanata Kiran wayar lawan a kashe ya fasa daura wannan auren  saida ta Sha ruwa ta dawo hayyacinta babanta ya kalleta dukanki akai haka ko likita ya gayamun na tabbatar lawan ne ya dakeki Dan Haka nafasa daura wannan auren ta Fara zunduma ihu karka rabani baba da babana Yana Raye dazemun abunda nakeso baya hanani farinciki na Banda uwa da uba sai Kai ka tausaya mun jikinsa yai sanyi lakwas nikike gayawa haka

Banzaci haka daga gareki ba Laila duk yadda narike nadaukeki a matsayin yata bana takura Miki mutane da dama sun dauka Nina haifeki Amma Zaki gayamun haka Mena rageki dashi indai aurene za'a daura Miki diyata nayarda zan aurawa lawan ke kuka tasa cike da tausayin baban nata kayi hakuri baba ka gafarceni Inasan lawan duk abunda zemin baze taba goge Sansa a Raina ba tabbas lawan ne ya dakeni Allah ya sawake bar kukan haka ya Isa kinji Allah ya shirya Mana ku dukanku yasa wannan auren ne silar shiriyar ku ameen baba

Washe gari ta Kama ranar daurin aure da wuri lawan ya farka ya tasheta tashi zan dawo Nan da karfe biyu ya Bata wadatattun kudin dazasu isheta ya fice gida yaiwa tsinke ya tarar har andan Fara zuwa dake adai dai dinsa yake suka gaggaisa da jama'a yashiga gida ya tarar da ummi zaune a tsakar gida tacika Tai dam ke Kuma lafiyarki cike da rashin kunya tafara magana latiyarce ta kawo haka banza yai Mata Dan yasan ko banza zataji ba Dadi yayi wankansa ya shirya yai tsaf dashi ya fito Yana fitowa ummi taga yadda yai kyau Nan da Nan tafara Bala'i dama gata uwar kishi wallahi ba inda zaka tadinga zuba ruwan rashin mutunci har maza suka Fara lekowa ya tureta ya saka soro mutane nata Bata hakuri ta shamma cesu saiji kuke cindim ta fada rijiya ihu mutane suka Fara lawan ya juyo Yana tambayar lafiya akace ummi ce ta fada rijiya mtswww yaja tsaki ku kyaleta ku wuce muje ba ita yar'iskaba zan nuna Mata nafita iskanci mace Bata juyani

Ya fice yabar gidan yaja zugar abokansa suka Kara gaba mutanen dake ciki duk daskarewa sukai a wajen cikin tashin hankali aka Nemo masu shiga rijiya suka shiga rijiyar suka dakko ta Tasha ruwa Tai zindim Bata numfashi Nan da Nan Mata makota sun cika gidan Dan sunsan zafin kishin ummi tausayinta suke Dan Bata Dace da Dan iskan Miji ba irin lawan Yana kallo matarsa tafada rijiya Amma ya fice ya tafi daurin aurensa hankalinsa kwance itako gata Rai a hannun Allah haka Amma ya wuce ya tafi Wai daurin aure Allah Kai Mana tsari da Miji irin lawan.

Nauwara ce ta keta bare bare Nan ummanta ta Bata wani rubutu Tasha ta wanke fuska tayi kwalliya me kyau ta fito tana fitowa ta karasa wajen alhaji ghali yasha babbar Riga kamar kullum ta durkusa ta gaisheshi ya amsa Yana kallonta kamar ya lasheta nauwara nauwara na'am alhaji bara na raka ka wajen mutuniyar ko ka wuce gidan nasu ai alhaji a'a dakata nauwara akwai muhimmiyar maganar danazo da ita kozamuje mota ido ta zaro a'a alhaji babana ze iya kasheni ya ganni a haka bara muje wanchan soron ta koma ta dakko sabuwar kakar innarta ta shimfida Masa a soron makotansu inda take zance

Suka zauna ta kawo Masa lemo daya Sha ruwan rubutu alhaji ghali ya gyara zamansa dama ba wani abu bane maganace akan maimuna na lura tun haduwar farko Bata Sona Bata kaunata ke Kuma kinban kulawa naji Dadi Dan haka zuciyata ke takeso kezan aura Dan haka banaso mudau lokaci me tsawo sunana alhaji ghali duk inda kikaga ansa g-samad textiles to nawane ido ta zaro nakane kwarai kuwa ya gyada Mata Kai jikinta ya Fara rawa wannan ne mashahurin me kudin dataji Ana maganarsa Yana cikin masu kudin Africa gaba daya yai murmushi karki damu inaso nagana da magaba tanki

Jikinta duk rawa yake zan sanar musu Baki bani number dinki ba wallahi Banda waya murmushi yayi zan aiko Miki yarana yanzu su kawo Miki sako suna waje suna jirana suna zaune aka kirashi tana Jin me ake fada alhaji gafa yaran ankawo dayan fari ne dayan Kuma wankan tarwadane inaga zasuyi basu wayar suka karba suka gaisa sai karyar da murya suke  maza ne dai Bata kawo komai ba yace da Wanda ya Fara  Kiran nasa kace su jirani Bata kawo komai ba Dan taji mazane may be yara aka kawo a company dinsa to nauwara zan tafi nayj Baki to alhajina kagaida gida Allah ya tsare nagode sai munyi wayar nagayama sanda zakazo

Dubu dari biyu ya Bata kyasha sweet firgita Tai Amma batace komai ba haka ta rakashi bakin lokonsu ta dawo gida jikinta Yana ta rawa duk ta gigice Bata Gama gigicewa ba Yara suka Fara sallama manya manyan ledoji aka Fara shigowa dasu leda bakwai ce cif suka juya tana kiransu Ina sun juya alhaji na jiranmu jiki na rawa umma ta jawo ledar farko atamfofine masu Bala'in tsada da less da material ta biyu jakunkuna ne da Takalma ta uku mayafaine da abayoyi ta hudu kayan kwalliyane masu kyau  ta biyar Mayamayaine da turarruka masu Bala'in tsada ta shida kayane irinsu cake kayan bakery dai da kaji ta bakwai din kayan drinks ne masu sanyi sai wata leda data janyo a ciki wayace a ciki kirara I phone x Dan itace waya me tsada ta karshe ihu tasaka ta rungume uwar suman hucin gadi tayi

Arziki kashi yata kin Tako me bala'in wari maza kwashi mukai ciki Kar babanki ya shigo duk da Dole mu nuna Masa wasu Amma ki boye wayar aiko suna Gama shiga sai gashi nauwara ya shiga kwala Mata Kira tafoto gani baba tana turo Baki waye wazo be wajenki dazu Naga an shigo da ledoji shine Wanda nakeso gidana ake shigowa da ledoji Toni ba makwadaici bane ki hada ki mayar Masa da kayansa kinsan nai Miki miji wallahi malam baka isaba umma ke fada wallahi bazakai mun bakin ciki ba in taso a wahala in Kare a ware yata ma ta tashi a wahala ta Kare a wahala wallahi baka isaba ai ba Kaine babba kanada Yaya wallahi shize daura wannan auren Haka kikace hakama na fada

Share hawayenki muje ciki suka wuce ciki tana ta fada wallahi bame takutawa diyata Haka ko akai Sam yaki amincewa taje ta Samu wansa dattijon kwarai tana kuka ita da Yar take Gaya Masa auren Dole ze Mata yasalam ai andena auren Dole yanzu nizan aura Miki Wanda kikeso dama nine waliyinki ki kwantar da hankalin ki zan neme shi zamu tattauna ki sanar dashi yazo zamu gana saina binkice Shi sosai cike da farinciki suka dawo gida burinsu ya cika hankalinsu a kwance

*ANAN ZAN DAKATA FANS KUYI MANAGE DA WANNAN SAINAJI COMMENT DINKU FANS NICE TAKU A KULLUM A KODA YAUSHE*

*FEEDYN BASH*

[10/3, 4:46 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *👳DAN ISKAN NAMIJI👳*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻

```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

19-20

Yayansa ya kirashi ya bashi hakuri ya nuna Masa yaran yanzu ba'ai musu Dole yayi hakuri ya Bata Wanda takeso yayi kukan bakin ciki bayan ya dawo gida wato be isa da iyalinsa ba kenan har Kara ake kaishi wajen yayansa yanajin kunyar yaron kwarai Bello yariga yai Masa alkawarin bashi diyar shi batare da yayi Mata wata wahalar lefw ba Dan yasan beda Hali mahaifinsa ya mutu sai mahaifiyarsa itama ba wada tacciyar lafiya ba shiyasa yakeso ya aura Masa nauwara
```

Dan ta dinga kula da ita shi malamin makarantar islamiyya ne iyakacinsa secondary saboda rashin wadata be cigaba ba kafin yai candy ya sauke alkur'ani da manyan hadisai yazama malami shiyasa ya ke koyarwa a islamiyya take wani tunani yazo Masa ya share kwallar idonsa alhamdulillah Allah yasa Tai min biyayya ita da ban hai fa ba

Malam Isa wan mahaifinta ya aika tazo yace yanasan ganin saurayin nata zasi mgn cike da murna takira alhaji ghali tagaya Masa komai yayi farinciki burinsa ya kusa cika yai aurensa ko hankalin mutane Yan bani na iya ya dauke daga kansa Dan wasu sun Fara zarginsa da neman mazan dayake yi Amma saboda temako da yakeyi yadda yake Basu kudi suka ja bakinsu suka kunshe suna fada sun San sun rasa to meyay musu zafi gwara suyi shiru Suma sa samu rabonsu duk da sunsan Dan luwadi ne Amma tunda baya bin Yara Yana lalatawa Basu damu ba dama unguwar ai kusan barikice bare shi me temako ma gashi babban mutum da kowa yasan shi

A Daren yaje ya samu kawun nata yai mamaki ganin kamar wannan mutum me mutunci da Kamala Amma ace kaninsa bayasan hada zuri'a dashi komeye dalilinsa oho nan ya Fara tambayarshi sunansa suna alhaji ghali nataba aure na auri matata ta farko wajen haihuwa ta mutu ta biyun ma ta mutu ta ukun ce muka rabu Allah be taba bani haihuwa ba Masha Allah bangaren sana'a fa dariya yai Ni Dan kasuwa ne inada shaguna a kwari da Kuma mall mall Wanda indai kaga ansa G-samad to nawane a zabure ya Mike alhaji Kaine Kai alhamdulillah ya akaji da jama'a ya temaki Nima ka taba temako na sanda nai ciwon kaba ka biya mun kudin aiki kazo asibintin abubakar imam kawo ziyara Amma ba'a Bari aganka Amma naji Dadi wannan ya tayi Dace Allah yasa ayi damu ya sanyawa auren albarka yasa yin na Allah ne ameen baba

Dama chanai bana bukatar adau dogon likaci wajen auren saboda nizan Mata komai yadda addini ya tanada kawai matar nake bukata Kai Kai alhaji ayi Haka anma Gama baba addinine ya tsara hakan mukuma bama iya aikatawa hakane dannan to inaso asa kamar sati biyu insha Allah gobe zan turo iyayena anyako ayi Haka anmayi anagama ka kwantar da hankalin ka baba bakai ne me daura Mata aure ba nine ai angama baba zasuzo da komai har lefen to Masha Allah ga wannan ayi hidima nagode zan aiko da komai daza'a bukata be kalli yawan kudin ba Kai madallah angode Allah yai maka albarka be duba kudinba Dan tsohone me dattaku ya rakoshi har bakin mota dake basu da nisa da titi ya dawo gida ya daga kudin meze gani dubu dari biyar ne salati ya Fara Yana salallami take ya Kira shi dama ya bashi lambarsa

Yana dagawa ya haushi da fada wannan kudin na meye sunyi yawa na gaisuwar iyayene baba

Kai da mahaifinta ne kayi hakuri karkace komai kyautace na baku Wanda ko bansanka ba zan iyai ma ita tabbas nasani base ka fafaba Dan Nima ka tabayi min Amma wannan neman aure kazo ba siyar ma da Yar zami ba a ransa yace Ni siyanta zanyi Kuma Dole kuse da mun ita nasani baba Kuyi hakuri kurike bayawa shike nan angode Allah yai maka albarka ya biyaka nan ya Kira mahaifinta da hanzarinsa ya hawo adaidaita sahu yazo Nan yayansa ya nuna Masa kudin zuciyarsa Tai daci dama abunda suke wa kenan Amma da Dan uwansa ya Gaya Masa ko waye sai yadanji sanyi aransa Amma kwanaki fa  yaji ana  ta rade radin Yana neman maza Koda yake mutane ba'a iya musu yake fada a ransa kodan sukashe masa kasuwane gashi zancenma yabi shanun sarki

Tabo shi yayi tunanin me kake ba komai Yaya Allah yasanya albarka Amma inda kwadayi da wulakanci kome ze biyo baya baruwana naji nasan da haka amma kasawa lamarin Allah albarka ai kagama magana Allah ze tsare tunda Taji tagani ba komai gobe ze turo iyayensa zamu karba nida makotana Tom Yaya zan tafi toga wannan tafi dasu haba dai Kai yabawa fa a a indai nine gaba dakai dauki kyauta nabaka kaje Kai hidimominka dasu Dan nasan Dole zaka bukacesu zan dauka yaya Amma wallahi saika dau wani abun a ciki kaji na rantse murmushi yayi ya zari dauri daya dubu dari yayi murmushi nagode Yaya da kyautarka Amma kyauta kaimun sai da safe ya rakoshi sunata hirar su ta zumunci ya kudiri niyyar shiyasan meze da kudin Amma bazewa wata yarsa komai dasu ba yasan me ze dasu

Arfan ne ya sakko shida nafeesat dining suka nufa suka tarar Maryam ta shirya komai yadda ya kamata sukaci abincin su hankali kwance Banda murmushi ba abunda yake har ya fita Bata fito daga daki ba ya yaje office ya cike abunda ze cike yai hotel din daya bar beb dinsa yana zuwa tundaga waje ake Masa kirari yaro da kudi abokin tafiyar manya kirari kala kala yadinga watsi da kudi ya wuce Kai tsaye har yanzu bacci take shegiyar Kaya ya fada fridge din dakin ya bude ruwa me sanyi karara ya dakko ya sheka Mata a firgice ta bude idonta zakici ubanki yau nizaki bawa wine tafi karfin kaina ko Dan kinaso ki tonan asiri ko zakici ubanki

Tun da yai arba da surar Maryam yaji Sam baya sha'awar Kara kusantar kowace mace sai ita wani masifaffen so yake Mata mara yankewa Nan ya jawo ta ya cire belt dinsa yadinga dukanta kamar Allah ya aiko shi tun tana ihu tana my love harta Dena magana sai hawaye sai da yaga tadena numfashi sannan ya kyaleta ya kunna Mata AC Dan ta farfado yai tafiyarsa ya barta a wajen Kai tsaye wani katafaren gidan sai da abinci yaje me Rai da motsi wato flavours yayo musu take away sannan ya siyo musu gasassun kaji wajen duk da akwai Amma ba irin wannan gashin ba me ruwa ruwa na Alhaji Mohd Malo yaja mota yai gida Dan yau jinsa yake sabon ango Dan Dole ya baje maitarsa a yau sai da yatsaya yase maganin dake sa zallar sha'awa sannan yase Wanda kesa bacci

Yaje yai parking sunyi mamakin ganinsa Dan Basu taba tunanin dawowarsa yanzu ba Nan Maryam ta mike zata wuce dakin ta a'a Maryam Ina zuwa meyasa kike gudun yayanki ne cewar arfan ba gudunka nake ba waje da zan baku no zoki zamanki sis ai duk daya muke tunda gida daya muke yanzu to Yaya  tadawo ta zauna ya zuba Mata ido sai kallonta yake itako duk ta takura itako nafeesat sai hira take zuba Masa umm kawai yake cewa anawata ga wata yake cewa a ransa gaskiya baze iya jira zuwa dare ba yanzu zeyi komai ta fanjama fanjam da yanzu da Daren duk dayane

Anty bara na Dora abinci no nasiyo Mana komai na manta dakko ki hada Mana abincin ta mike ta Debi ledojin ta shirya dining wata dabara ta fado Masa Bara nadan watsa ruwa ya hau sama sai ya watsa ruwa ya bar wayarsa Yana sane ya zira jallabiyya ya sakko shi kawai suke jira Nan yanemi gu yazauna aka Fara ci ta tsiyaya musu wani mist fruit da ake sedawa me bala'in Dadi a glass cup dama ya zuba magungunan say aljihu Nan yaga sun Fara Sha musamman nafeesat dake tana mugun San ta cikin hanzari Dan karsu shanye yauwa nafeesat maza dakkon wayata a sama tana mikewa ya kalli Maryam yai murmushi kanwarmu dakkon fura a fridge ki hadon da apple Amma Dan Allah ki yayyanka ta to tace dandama batasan kebewa dashi tunda ita tasan halinsa murmushi ya saki ya sawa nafeesat kwayar bacci a lemon ta yasawa Maryam ta sha'awa a lemon ta yadda ze samu gamsuwa bazata wahalar dashiba

*To fans sai naji comment dinku masoyan Dan iskan namiji adai Kara hakuri nice taku a kullum akoda yaushe*

*Feedyn bash*
[10/3, 4:46 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *🧑‍🔧DAN ISKAN NAMIJI🧑‍🔧*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Wannan page din Sadaukarwane ga latest novellas by samee Ina fatan Allah ya temaki wannan group me albarka inajin dadin kulawarku da comment dinku nagode sosai Allah ya Kara Mana Amana da zaman tare*

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DA SUNAN ALLAH ME RAHMA ME JIN KAI GODIYA TA TABBATA GA ALLAH UBANGIJIN TALIKAI TSIRARA DA AMINCI SU TABBATA GA ANNABI MUHAMMAD SAW*

21-22

Nafeesat ce ta Fara dawowa ta kawo Masa wayar ta zauna sai ta hango na arfan yafi nata yawa dabara ta fado Mata la Yaya kaga wani news Yana juyawa ta dauke nasa ta maida Masa da nata ta kyalkyale da dariya tsokanarka nake shima dariyar yai nafeesa bakya rabo da zolaya Wai Ina Maryam ne na aiketa kitchen ta yankon kayan fruit be gama rufe Baki ba sai gata Yana cin abinci cin da kyar ganin Maryam Taki sha Amma nafeesat ta shanye sai da tagama ta shanye tasa sannan hankalinsa ya kwanta har wata ajiyar zuciya ya saki lafiya ko dear ba komai sweety ya saki murmushi ya Kama cin abincin haikan ka'in da na'in sai da yaci ya koshi yadda zeji dadin aikin tukun ya daga lemon ya kwankwade
```

Yana lasar Baki cike da farinciki muntinsa biyar da Gama ci sun koma parlour suna kallo maryam ta shige daki Arfan yafara doka hamma bacci me nauyi ya Kama shi tuni ya Fara gyangyadi ganin haka nafeesat ta Kama shi da kyar Dan har yafara tangadi bacci yake sosai lafiya Wai dear nafeesat bacci kwantar Dani da kyar taja shi dakinsa na kasa ta kwantar da shi tafita taiwa maryama sai da safe Dan itama bacci take ji dama ita gwanar bacci ce suka wuce ta kulle dakin ta kwanta jikinsa Amma Ina kamar gawa kawai bacci yake bema San metake ba ta tabashi taga kawai sakin munshari yake to shi wnn lafiya wnn bacci haka Tai kwanciyar ta

Ita ko maryama ta shiga tashin hankali bala'in Sha'awa ce ta taso Mata gashi Bata San yaza Tai ba kawai namiji take bukata haka tadinga murkususu tana ciwon Mara tana matse cinya Bata saka hannunta ba Sam Dan tasan haramun ne duk tsananin Sha'awar datake ji haka ta daure gumi kawai take ko Ina jikin ta rawa yake take tayiwo alwala ta tada sallah a haka akan daddumar bacci me nauyi ya dauke ta gaba daya ta gama jikewa da gumi jagab Tai ta wasu irin mafarkai gashi Nan arfan Yana binta da gudu sunata gudu chan sai kawai taganshi a gabanta Yana wata dariya bazaki taba tseremun ba ke tawace hhhhhhh haka Tai ta mafarkai sai bayan magriba ta farka duk ta jike da gumi Tai salati ta sanar da ubangiji

Ta shiga Tai wankanta ta dauro alwala tana ta addu'oi Allah ya tsareta daga sharrin arfan Dan Wallahi masifar tsoransa take ita Wallahi tana tausayin yayarta da Allah ya hadata da Dan iskan namiji nafeesat saliha ce itako zata tambayeta garin Yaya suka hadu da wannan mijin nata duk da tana tunanin rabo ne inba haka ba Ina ita Ina shi a haka tafito parlour tana ta tunane tanane taga wayam basa Nan take ta Fara gyara ko Ina na gidan ta kunna turaren wuta wani Ni'imtaccen kamshine ya ziyarci hancinsa Yana tsaka da bacci a hankali ya bude idonsa meya faru dashi a sukwane ya mike

Yaga nafeesat na bacci itama dama ita mayyar bacci ce ta shinta yai nafeesat ya akai na kwanta bacci me nauyi haka ta mutstsike cike da magana irin ta masu bacci wallahi baccine ya dauke ka daga Shan lemo kadinga bacci da kyar na shigo dakai dakin Nan saboda bacci jikinsa har rawa yake garin Yaya Haka tafaru ya furta a ransa biki Sha lemon ki bane na Sha Mana wayo naima nasanja maka da nawa naka yafi yawa na dauke naka sanda nace ka juya dinnan sannan na dauke gyara kwanciyar ta Tai ta cigaba da baccin ta mtsww wani masifar tsaki yaja ya fada bandaki yai wankansa yafito yasha kana Nan Kaya sun Masa kyau ko kallonta beba ya

fice Dan ya tsaneta ita ta janyo Masa tafka wannan asara

Yana fita falo sukai ido hudu da Maryam tana kallon wani American film a fox series Banda tabe tabe ba abunda ake itako sai matse matse take ido hudu sukai shibe sauke ba ita Bata janyeba bala'in burgeta yai Dan ba karamin Sha'awa takeba daya akesawa shi hudu yasa Mata Kuma ita bazata taba sabawa mahaliccin taba wannan ma Dan film ne da hanzari ta mike cike da kunya yadda take kallonsa ta kashe tv din ta nufi daki Maryam ya kirata da wani whisky voice sumane kawai batai ba dawo ki kallonki fita zanyi

Ko motsi ta kasa yi Dan yagama kashe Mata jiki da muryarsa ganin Haka ya karasa ta jawota jikinsa ya hadesu gu daya ta kasa ture shi ta kasa Hana shi jikinta ya mutu kawai so take tajita ajikin namiji (hattara iyaye da yammata wallahi akwai wannan kawayar a gaske Wanda da ita ake amfani ake karbewa yammata budurci musamman masu kwadayin cin abun hannun saurayi yakamat iyaye mu hankalta da yammata)ya matseta a jikinsa ya hada bakinsu gu guda yadinga kissing dinta tuni ta sakar Masa jikinta gaba daya duk sunfita daga hayyacinsu motsi yaji alamar nafeesat ta tashi ya tureta ya fice da sauri zubewa tayi a wajen ta saki wani uban Kuka tana ihu baba ka cuceni aure nakeso wallahi da gudu nafeesat ta fito

Guri ya cika an taro yayi taro andaura auren lawan da Laila Amma amarya na gadon asibiti ango Baki kamar gobar auduga abokansa mamaki suke sunzo gulamane kawai bawai daurin aure ba ko a mafarki basiyi tunanin za'a aura Masa Laila ba sai gashi a gabansu aure ya dauru bayan komai ya natsa babanta ya Kira lawan da yake tsaye Yana jiran amarya ta fito shiga kwallon Dan iska ya tsuguna baba gani baba ya Soma bayani kamar Haka alhamdulillah Allah nagodema na sauke nauyin daka doramun na aurar da Laila nauyi dayane ban sauke ba ban zaba Mata mijin da ya Dace da itaba Wanda addini ya tanada

Koda yake kaddara ta Riga fata Allah yayi rabonkace matar mutum kabarinsa Amma lawan ga Amana Nan banine mahaifin Laila ba hhhhhh Aina sani bava cewar lawan Kai yayan babantane to ai kakarta ma data haifi babarta ba'asan ubanta ba ita kanta babarta sai da ta Dan eh ta zazzaga sannan ta auri Dan uwanka aka haifi Laila da kannen ta Dan Haka Banga abun daga hankali ba baba nine daidai da Laila duk Dana San wannan Sirrin Amman na rufa Mata asiri na

aureta baba karka manta duk yawon Nan Laila ma nadan zagawa Kuma Yar giyar Nan tadan Sha saboda masifar Sona da kishina Dan Haka baba kabasar kawai nida Laila mutu ka rabane auren zobe mukai baya mutuwa matsalar daga itane fa kishi Ni kima zuciya Dan haka aja mata kunne ta gidama hakuri take Dani

Baba yagama mutuwar zaune Dan baze iya cewa komai ba game da wannan tantirin tunda beji kunyar tarar sa da wannan maganar ba ya tsaya ma bashi amsa shima yazama mahaukacin maganganunsa ba karya Amma a Ina yaji ko Laila tagaya Masa Kai Ina itama batasan da wannan ba Amma wannan yaro Dan iskane yasan da Haka Amma ya dage sai ya aureta gashi an daura itama ta dage baba kadena tunani nibanwa yarku asiri ba hakanake da shiga Rai shiyasa Mata suke mutuwa akaina ya Mike zan koma baba to lawan Ina Laila tana asibiti yai Masa kwatance ya fice shiko mutuwat zaune yai be Kara magana ba

Yana fita sukai asibitin shida abokansa tana kwance fuska yai zindim nad da bandage yadanji tausayinta besan Haka yai mata ba ya rungumeta yadinga lailayata abokan suka tafi suka barsu sai murna take Yan gidansu ko sai sha'awa suke Basu ba Wanda yasan meya wakana sai baba shiko tausayin Laila yakeji tanada biyayya ga kyauta Allah ya jarabceta da Dan iskan namiji sai yamma ya tafi zeje gida ya dawo a asibitin ze kwana da ita Dan soyayyace ake yinta a ranar Bata wasaba saika rantse da Allah lawan ki tsawa baze iyayiwa Laila ba tsabar kulawa(Allah karabamu da Dan iskan namiji me Hali irin na lawan zulwajihaini wallahi akwaisu life irinsu)

Ya ja motarsa sai gida ba kowa a gidan kowa ya tafi sai yaransa sai ummi data gama cika Tai Dan ta hada kayanta komai a gefe shi kawai take jira Taji dirin motarsa sai gashi ya shigo Yana zukar sigarinsa Yana dariya mezan gani ummi yaji Zaki sai kin jirani ai Naga inza ai yaji ba'a sallama da Miji ranta ya gama baci eh dama saboda danka bansan nabarshi yai ta garari shi kadai a waje hehehehe Ashe Ana Sona tunda anasan jinina mtswww Allah sittiri bukwi mezan da Dan giya manemun Mata Dan iska irinka ransa ya baci nikike gayawa Haka Dan Kinga Ina kyaleki agidannan darajar yayanmu nafada banza Dan iska gadan gadan ya nufeta itama da zafin zuciya Taki gudu ya shaketa

*To my fans inje ruwan comment kawai kuji ruwan typing nice taku akoda yaushe uwargida a gidan bash*

*Feedyn bash*
[10/3, 4:46 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *💆🏻‍♂️DAN ISKAN NAMIJI💆🏻‍♂️*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*ASSALAMUALAIKUM WANNAN PAGE DIN SADAUKARWANE AGAREKI MUMMY ILHAM YADDA KIKE KAUNAR WANNAN BOOK DIN DAMA DUKA BOOK DINA NAGODE ALLAH YABAR ZUMAUNCI YA BARA KAUNA KIYI YADDA KIKESO DASHI NAKINE KE KADAI INKISO KIHANA KOWA KARANTAWA😉😉😉😉*

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DA SUNAN ALLAH ME RAHMA ME JIN KAI GODIYA TA TABBATA GA ALLAH UBANGIJIN TALIKAI*

23-24
```

Dan ubanki nine Dan iska ya shaketa dakyar take fitar da numfashi yayan sai kuka suke suna ture uban daga jikin ta sai dayaga tadena numfashi ya saketa a kufule ya shige dakinsa ya kunna sigari ya dinga dankarawa cikinsa Amma batai Masa ba tuni yafara Mirza wiwi da hanzari ya Fara zuka cikin gwanan cewa sai sannan ya Fara jinsa ya koma normal wallahi bazan dau iskanci ba data fada rijiyar ubanwa ya cirota mtsww yaja tsaki

Ummi ko tuni idonta ya firfito waje numfashinta ya dauke Dan ba karamar Shaka yai Mata ba cikin ikon Allah babbar me suna Zahra tayi dabarar debo ruwa sunata zuba Mata Banda kuka ba abunda ragowar sukeyi cikin ikon Allah ta farfado dakyar ta mike ta rungume yaran tana kuka suma suna ta kuka tabbas tayi kuskure sone taja Mata aikata wannan kuskuren shiyasa annabi yace kunemawa Yaya yenku uba nagari ita yanzu mezata dorar a rayuwarta da lawan najin Dadi sai dai soyayya kawai

Haka ta wuni kuka ta Debi kayansu ta maida daki dama kawai barazana Tai Masa ashe rabon taci dukane bayan rijiyar data fada akansa Amma ko akikinsa itama Kuma aranta batajin zata sauke wannan kishin datasawa kanta andai daura aure sai tariya taga shegiyar dazata shigo Mata gida wallahi ba wadda zata shigo gidannan a matsayin kishiya gidan tane ita kadai Dan ita lawan yai wannan gidan

Ita fa wallahi da kishiyar gida gwara ta waje tunda Bata ganiba batasan da zamanta ba Amma wallahi zata nuna Masa ta fishi hauka wallahi sai ta bargidan Bata Isa tazauna Mata a gida ba tana Nan tana zuba idon ganin ranar daza a shigo Mata da amarya haka ta dinga saka da warwara a kwance Dan zazzabi ne me zafin gaske ya rufeta tanajin sanda lawan ya fito ya fice koya lekasu kuka ta saki me ciwo

An kawo kudin auren nauwara million 1 an kawo lefe akwati ashirin da hudu da mukullin dankareriyar mota kawunta zaucewa ya kusayi Shiba siyar musu da ya zeyi ba sukayi dariya ai

su burinsu alhaji ghali yai aure Kuma wnn ba komai bane cikin dukiyar alhaji ghali matar daze aurace kome yai Mata Basu Fadi ba Nan suka ishe shi da dadin Baki aka tsaida Rana sati biyu dama kayan lefen suna cikin motar tata sun Gama tsara komai da nauwara da alhaji ghali komai na gida yace baya bukata akwai komai

Suna tafiya kawu yasa aka kirawo Masa dansa ya shiga gaba yaja motar bayan da boot din shake da akwatuna wasu kan wasu sai kofar mazugal gidansu nauwara sunayin parking yasa aka Kira masa Yara suka dinga jidar lefen suna kaiwa gidan tun suna mamaki har suka tsaya suka zubawa sarautar Allah ido kawune ya shigo ya Mika musu mukullin motar da zunzurutun kudi naira million guda kudin auren nauwara Wanda tunda suke a duniya Basu taba ganin kudi irin haka ba

A take umman ta ta sume itako kuka tasa na farinciki da tsoro Anya ko bataiwa kanta zari ba Bata Kai kanta inda zata halaka ba kuka take wiwi ta debo ruwa ta zubawa umman tata malam ya fito ya kalli kayan gabansa Banda faduwa ba abunda yakeyi wannan tsabar dukiya a gidansa sunan kayan auren diyarsa da wane ido ze kalli mutane ta tabbata ya seda yarsa kawu ne yace to malam ga kayan auren diyarmu da kudin auren ta million guda da mukullin mota har laude since ingaya ma Ba'a bukatar komai na kayan daki Dan haka sun yafe

Malam ransa ya gama baci jijiyoyin kansa sun tashi sunyi rada rada kawu wallahi bazanyi kaffara ba ba hannuna a wannan auren suyi duk yadda sukeso Amma duk abunda ya biyo baya wallahi ba ruwana tunda yata tagaza yimun biyayya Yana matsar kwalla su kwashe kayansu su fice mun daga gida ke Kuma bakin cikin da Kika sani a bakin da hanzari kawu ya toshe Masa Baki haba bansanka da irin Haka ba kafa sawa abun albarka wallahi na janye banyi tunanin abun ya Kai Haka ba yaya dama Kai ka karbi auren Nan duk abunda ya biyo baya su nemeka

Kawu ya rike hannunsa suka fita yanata rarrashin sa yace ya janye sakin dama be furtaba su zauna a gidan Amma baruwan shi da sabgar auren su shima yanada tasa sabgar shikansa habu Dan gidan malam ya girgiza da ganin dukiyar shikansa yaso nauwara Amma yasan tafi karfinsa Haka suka fito suna maida yadda akayi umma ta Basu dubu dari da kyar kawu ya karba Yana fitowa yabawa malam Dan Yana tausaya Masa shi yanada Yaya maza manya suna

Ya dawo ya zaro nonon ta ya Fara Sha ta Kara tura Masa habawa Nan da Nan ya chafe wata Kara take da ihu dayaga shima ze fita hayyacinsa tuni ya dauke ta kamar baby yai dakinsa da ita yai Mata tik lungu da sako sai daya Gama sideta sannan ya Fara lalubar hanya Nan fa tace Bata San zancen ba Dan wani bala'in zafi daya ratsata nidai da gudu na fito Ina hawayen tausayin Maryam Dan nasan me afkuwa ta afku wannan tashin hankali har Ina

Bayan minti talatin naji maryam mata ihu tana dukan arfan shiko ya rike ta Gam yanata shata tatar hawaye wallahi Maryam kozaki kasheni bazan iya rabuwa dake ba kece rayuwata inasanki Maryam so na gaskiya bantaba sanin cewa Mata suna suka Tara ba sai akanki zan iya rabuwa da kowa da komai akanki kuka yake kamar karamin yaro Dan ya gamsu dama Haka wannan kayan take chab wallahi baze iya barin Maryam ba sai dai ya rabu da yayarta wallahi akanta ai ya halatta tunda ba tare ya hada su ba gaba daya ya fita hayyacinsa Maryam bakin ciki ya gama tokare Mata zuciya gata cikin jini yau wani Wanda ba mijinta ba ba uncle din ta ba ya karbe budurcin ta amatsayin ta na budurwa Kuma Wai mijin yayarta mafi soyuwa agareta Ina

zata Kai wannan abun kunyar

Wallahi arfan Kai Dan akuyane dan bunsuru kaci yaya kaci kanwa wallahi kobance ma komai ba Kai kanka kasan Allah baze barka ba Dan baya zalunci burinku ya cika Kai da abba na dama nasan abunda kake so kenan amma kanka kaiwa Dan banga lefin ka ba babana shiya jazamun da bebi zarmewar zuciya ba yayi hakuri da abunda Allah ya bashi yai min aure kamar yadda na bukata daban baka hadin Kai ba nasan Nina kawo kaina gareka arfan bakai mun adalci ba na tsani kaina na tsani rayuwar duniya da abunda ke cikin ta ta kifa kanta tana gunshekan kuka

Astagfurullah Allah na tuba da wane ido zan kalli ubangiji nice da Zina Ni Maryam wallahi na tabbatar wannan shine tikitin shiga ta duniya Banda wani sauran mutunci bani da shi zanta rayuwata a Haka arfan na zabi rayuwar da kuka zabar mun Kai da babana tausayi ta bashi ya Mike jikinsa yai sanyi lakwas ya rungumeta shima kukan yake kiyi hakuri Maryam kaikayi ne ya koma kan mashekiya na dauka kema kamar sauran Mata kike Ina gamawa na Gama dake Amma sanki a Raina yake Maryam inasanki ki yarda Dani Dan Allah shiru tayi ita Kuma Bata kwace jikin taba

Alhaji ghali duniya sabuwa sababbin company ya bude a Dubai Dan sun Shana shida amaryar sa baby Chakwai yau ne suke sa ran komawa kasar su ta gado domin yau ne ranar da aka daura Masa aure da amaryarsa wadda Bata gaban shi babban burinsa baby Chakwai Kuma yayi nasara Dole Yan kungiyarsu su kiyaye shi yadda ya shawo kan baby Chakwai har sukai aure shiyasa yanzu kowa  so yake yaji meyaiwa baby Chakwai yadda ake ji dashi daga gida har kasashen ketare saboda yadda yake gamsar da duk Wanda suke tare ya iya aiki yadda ya kamata badan ransu yaso ba suka shirya suka taho Kano Dan an shirya musu hadden party a Daren inda za'a raka baby Chakwai gidan alhaji malamalai da sunan amarya kamar yadda al'ada ta tanadarwa ko wace amarya

_To fans mu hadu zuwa gobe dan jin yadda zata Kaya tsakanin baby Chakwai da nauwara maji ma gani nice Taku a kullum a Koda yaushe_

*Feedyn bash*
[11/11, 9:38 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *💁‍♂️DAN ISKAN NAMIJI💁‍♂️*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_Assalamualaikum my fans Dan Allah Dan annabi kudena cemin ga yadda zanyi na Riga na Gama tsara labarina bana San katsalanda a lamarina gwara idan shawara ce ki bini personal private kimun magana bawai kidinga cemun be kamata arfan yaiwa Maryam kaza ba yadda kukeso za'ayi darasi nakeson bayar ba bawai san Rai ba wayanda suka fuskanci inda na dosa alhamdulillah so Dan Allah banaso nagama tsara labarina Dan ko rabi ban ba idan Kuma Naga yayi worst zan dakata rubuta novel din harda masu Bina private Wai be kamata nasa yai galaba akan maryam ba shin salihai nawa ake batawa Koko kowacce Yar iska ita takai kanta_*

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

51-52
```

Haule suka nemi waje suka zauna ita da jama'ar ta meena ta samu nauwara ta sanar Mata da zuwan su haule fitsari me kawai batai ba saboda tashin hankali Bata taba tunanin haule da gaske take ba wallahi da gwara ta Sanja event Tai asarar 1.5 million din da aka Kama the affiecent din tunda ba ita zata biya ba Bata da asara meena ce tadinga kwantar Mata da hankali sannan ta nutsu biki yayi biki Kowa shi ze zuba abunda yakeso yaci San ransa kaji ne tuwo ne fried rice komai gashi Nan

Nan mc ya Kira amarya tsakiyar fili ta fito ya nemi kawayenta si Mata Kara suka Sha rawa har amarya dasu liki haule ko taci abinci kamar me ta Lodi kaji tasa akai Mata motar dasu kazo cikin ikon Allah Basu hadu da hajiya ba duk da zage zagen da ta dunga yi ba Wanda ya kulata a wajen aka nemi uwar amarya ta fiti bayan kawaye sun koma Nan fa kallo ya koma sama chan na hango su nerner Aysha dasu mummy ilham sun biyo bayan haule indaga ido na gano su maman auwal dasu fauzeyyer a bayan hajiya cogal cogal haule ke tafiya kafin ta farga hajiya taiwa fili tsinke Nan ta rungume nauwara my daughter habawa sai hotuna Nan aka Fara barin liki fili ya rinchabe

Sai ga haule ta karaso ta bangaje hajiya daga jikin nauwara shegiya munafika annamimiya Allah yai wadaran ki maida Dan wani naki sanda nai wahalar nakudar kin tayani ko kinsan San da nai a inama nasanki saboda Kinga dukiya Zaki makale gashi da karfi take maganar kowa naji hankalin kowa ya dawo kansu ganin wannan drama ita ko amarya sai kifta Ido take kunya ta isheta ita ma hajiya da karfin Hali ke malama ice ko Baki da hankali ne ko kin Sha kwaya ne Banda mahaukaciya ce ke ki kalle ne kice yarki haba wa waje ya rin chabe da bala'i anrasa me gaskiya cikinsu

Hajiya ta fusata ta waskawa haule Mari ta hankada ta ji kike kas kafa ta karasa gurgudewa ihu tasa talatu me kuke jira ihu haule take sosai Dan azaba takesa da gudu suka fita suka jido kayan aiki habawa masu gadi na ganin Haka sukai ta kansu suna shiga suka farwa hajiya da makarraban ta wasu Kuma suka Fara kan me uwa da wabi kafin kace kwabo annemi kowa anrasa kowa ya gudu amarya ma ya samu nata rabon a goshi ya fashe hajiya ko raga raga sukai Mata sai jini ke zuba suka kwashi haule suka gudu suna fita sai ga Yan sanda sun shigo aka kwashi su hajiya da wayanda suka jikkata akai asibiti dasu

Direct gida suka nufa suna zuwa a ka Kira me gyara sabon dauri akai wa haule harda Kashi gudawa dama taci yafi karfin cikin ta kowa ya tausaya Mata kuka take tana kwashewa nauwara albarka Dan ta Gama Bata Mata Rai mutane keta rarrashin ta Akan tayi hakuri tayafe Mata aka Kira malam aka Gaya masa yadinga bala'i yace da izinin wama ta fita shima hakuri aka dinga bashi ya fice yabarta a wajen abun duniya yaiwa umma yawa ga bakin cikin nauwara gana ubanta na uban yafi damun ta saboda tunda yai wannan auren bashi da lokacin ta

Ankai su nauwara asibiti an sa Mata bandage inda hajiya take ta bala'i wallahi bazata yarda ba sai anyi bala'i nauwara lallabawa Tai suka gudu ita da meena dama meena ce ta samota itama hanyar ta akai Mata Bata San gidan su kowa ba a cikin su suna zuwa suka tarar umma na sauke kwandan jaraba tace sai dai nauwara ta koma inda ta fito gidan uwar data sake wadda ta fiti mutane ne Yan uwan umman Yan biki suka dinga Bata hakuri har kuka Tai sannan zuciyarta Tai Mata sanyi dan ta fusata da nauwara Haka aka dinga Baki akan tayi hakuri tasa Mata albarka ta sawa auren albarka daga yaune dai haka ta hakura aka shirya ta Yan uwan haule

Bayan daurin aure da yamma maimunatu akai yini nata Dana umman ta alhamdulillah komai ya wadata anci ansha kowa yai farinciki bikin su day dai na talaka suka yi ba wani tashin hankali bayan magriba Yan uwanta suka shirya ta suka sa Mata Kaya masu kyau atamfa ce me tsada suka nadeta da laffaya  tayi kyau da kafa suna tafe ana wakoki abun alhamdulillah cikin tsari suka tafi aka kaita gidan ta aka damka amanar ta ga dangin mijinta uwar mijinta tayi murna ta rungume ta tana farinciki da wannan kyauta da Allah yaiwa Dan ta mutane sunyi mamaki sun gigice hankalinsu ya gama tashi Yan bakin ciki nayi Yan hassada nayi kowa da kiwon daya karbe shi masu farinciki ko ba'a magana Dan maimuna ta samu masoya alhamdulillah anyi biki Ify angama Ify Allah ya bada zaman lafiya

Alhaji ghali ya diro a Kano shi da baby Chakwai hankalinsu a kwance sun gama shirya yadda komai ze kasance za'a rako shi anjima a zuwan abokan angone suka kawo shi Dan ai Badda kama suka rabu ya tura gidan su nauwara da manyan motoci na alfarma Wanda wasu sun firgita hankalin su ya tashi ganin motocin kawai bama suje gidan ba sun gani Yan gulma kowa fitowa yake Amma motoci sunki karewa kamar ma Dado su ake anbada amarya kema gas ko kukan Nan na al'ada fuskarta a bude.

_To fans maji ma gani sai Allah ya kaimu gobe maji inda aka kwana Allah yasa mudace nauwara a gidan alhaji ghali koya Labarin lawan ku biyoni gobe danjin yadda zata Kaya nice Taku a kullum a Koda yaushe_

*Feedyn bash*

[11/12, 7:55 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *👳DAN ISKAN NAMIJI👳*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻

```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Bismillahir rahmanir Raheem*

53-54
```

Nan shegumi ya Fara tashi wannan fitsara dayawa take kuduba yadda aka tafi da Maimunatu tana risgar kuka da kyar aka bambare ta daga jikin uwar ta Amma ita wannan ko tari ta tsaya ma ai Mata fada sai chatai mezata ji yi nayine Bari na Bari bayau tasaba jiba Kona kawaye ai ta dauka Haka ta shige mota bako kunya duk Wanda yaje Kai amarya karyane yace be samu mota ba asake a wale mutum uku baya gaba daya Haka suka dauki hanya zuwa dambare kowa zuciyarsa cike da gulma

Anzo gidan amarya layin gidan ta na opposite buk new side ba wahala gidan ta motoci suka dinga shiga wani hangame men gate duk yawan motocin Nan sun shige ciki Nan fa kallo ya koma sama mutane suka Fara sakin Baki suna kallon ikon Allah Basu tsinke da lamarin ba sai da suka shiga gidan Nan duk wani nothing kansu ya gama kwancewa parlour ne na haduwa sama da kasa ne gidan tsayawa Gaya muku haruwar gidan sai na cika wannan page din gida yai gida komai enough mutane Yan gulma sun nade komai
wasu ko tsorata sukai kodai Dan yankan Kai ne Inba haka ba wannan daular ai Dole yace bayasan ko tsinke Ina zasu sa shirgin su

Su kan su jikin su yayi sanyi Amma wayanda suka San shi basuyi mamaki ba Dan ginta sai zubar da habaici suke Yar su me goshi bame kashin tsiya ba da Indo suke Dan tazo suka karaci rashin mutuncin su aka ce kowa ya fito za'a tafi saboda dare ya Fara yi kowa ya fice aka bar kawayenta wani abokin alhaji ghali ya shigo mezan gani kunsan da nisa Kuma mu duk anan muke muna Kai ku mundawo gida a haba wallahi ba inda zamu sai munyi siyan Baki ya zaro ido meye kuma siyan Baki andade da denawa ai to wallahi mu sai min siya to nawane Kuka siyar suka yi far da ido ko wacce sai karairaya take lallai sai yaga wata Yana so Suma su shiga daula

Yai murmushi ku fada man dubu dari biyu cewar meena yai murmushi yace Ina zuwa yai waya sai ga shi an shigo Masa da jaka basu dubu dari biyar ka mayar mun mota jiki na mazari driver din ya Basu gaba dayansu suman zaune sukai dakayar Mai kyau Tai kokari ta karbo kudin to muje ai da sauri suka mike ko wacce tama Mai ta rada wannan tace goho wannan tace gicciye suka dai yi tayi Mata radar shakiyanci suka fice shiko dariya ma suke bashi yasan duk Dan shi suke ta wani iyayi da karairaya shiko mace Bata ma burgeshi tashi ma ta gida hakuri take da shi sai sanda rabon haihuwa ya rantse ake samun cikin shine ze kusance ta

Ki koma daki a a kaje gani Nan cewar meena yanzu zata koma Kinga ki koma daki yanzu ta rada Mata Amma da kinji shigowar angwaye ki dawo parlour karki sake wani gardi ya shigar Miki bed room bare har yaga makwancin ki Tai murmushi ta rike ta ta maida ta dakin sai da yaga ta shiga hankalin sa ya kwanta meena sukai sallama a zuwan sai gobe zasu zo budar Kai bayan kowa ya watse ta cire mayafi ta dinga zagaye gidan Suma ne Bata ba Dan Dadi wannan dukiya gaskiya ta Dace a duniya saura lahira Haka ta gaji har sama sai da ta hau ta dawo daki ta Kara fesa kwalliya tasaka turaren jaraba ta Kara bankar magunguna jira kawai take komai ya kammala ta fito ta dawo parlour sai sannan aka wani jawo mayafin munafinci aka rufe fuska minti goma da zamanta ta Fara jiyo hayaniyar mutane ta Fara gyara Zama

Sai me Buda Taji anshigo da ita hehehe Allah ya kawo mu ayyiriyiri shigo a hankali amarya baby Chakwai uwar gida sarautar gida duwawuce ke Dole a zauna dake makiyan ki fadawan ki Wanda yai Miki iskanci ke kadai kikasan mezaki Masa hehehe da sauri ta bude lullubin mezata gani alhaji ghali ne sakale da wani Dan siririn saurayi kyakykyawa dashi kafar shi Tasha kinshi Haka hannunsa ya zuba zobuna kafa da hannu da wuya sai balle dollar ake Ana musu liki ba Wanda yabi yakan kwasa sai masu wannan kirarin ido ta zaro waje alhaji mezan gani Abu banbara kwai namiji da suna hajara waye wannan Kuma Naga ka sakale shi kamar zaka Mai dashi ciki zuruf marokin yayo gaba sa minjaye hajiya

Yadda kike jinki mace haka muke Jin kanmu alhaji ghali Zaki iya Kira namiji Banda amarya Sha guda baby Chakwai yarinyar da ake yayi gida da waje inbaki yadda ba muje ciki a dubaki a dubamu idan da wani bambanci sai ki fada Ido ta zaro cikin in Ina wa...wa...cece wannan din hehehe uwargida Kenan tauraruwar alhaji ghali yarinya me yayi me tsada wadda aka dauro auren ta a baban birnin duniya wato America innalillahi wainna ilaihirrji'un Kenan kanaso kace min auren Jinsi kwarai ko Amma ita fa baby Chakwai ta Dade a macece kamar ke ehe

To sarkin zuba chakwaikwai wa ya Isa bamu gu muzauna suka zazzauna ita ko ta kasa Zama hawaye kawai take yi Yana nadamar abun da ta aikata inama inama inama hannun agogo ya koma baya data barwa maimuna shi dama ita yake so zauna cewar alhaji ghali da kyar ta zauna a dosane yayi gyaran murya ya Fara jawabi kamar haka nauwara inaso kisan da cewa banyi aure Dan inzauna dake ba nayi aurene a matsayin ki Zama garkuwa a gareni yadda bame

zargina koya zargi gidana bansan zuwa hotel saboda Ni babban mutum ne bansan inta kwashe kwashe saboda inada kyankyami shiyasa na yanke shawarar auran baby Chakwai wadda dama min Dade muna soyayya muna San junanmu

To alhamdulillah munyi auren so da kauna karki tunanin inasanki wayan Nan duka abokai nane suna da damar zuwa gidan Nan asan da suke Banda shamaki tsakanina dasu ke Koda ko ke suke bukata zan Basu dan kudi nasa na siye ki Abu daye ne bazan iya Basu ba baby Chakwai ya rungumshi saboda Chakwai din fa akwai Chakwai yayi wani far kamar macen gaske ya Sha make up Nan parlour din ya kaure da sowa suka dinga surutan da Bata fuskanta Dan ta Gama Suma Ita tunda uwarta ta haifeta Bata taba ji ko Labarin ganin iskanci irin wannan ba yaci gaba da magana zaman lafiyarki a gidan Nan yiwa baby na biyayya baby fada Mata abun da bakyaso

Ya wani gyara Zama Yana rangwada abunda banso guda daya ne Koda Wasa karta kuskura ta rabeka Dan inada masifar kishi musamman akan abunda nakeso zan iya kashe ta akanka ihu nauwara tasa kisa tana ta rusgar kuka kamar ance uwarta da ubanta duk sun mutu yaci gaba dama dokar gidan Nan ba Yan aiki duk girman gidan Nan ita zata share Tai moping Haka zalika bawa shukoki ruwa idan Kuma wani daga cikin Ni ko alhajina ze fita Zaki wanke Mana mota ki bude get idan zamu fita bansan jiran girki ki tabbatar kin Gama abinci kafin na tashi kiyaye dokokina shine zaman lafiyarki villeger Yar matalauta kawai mtsww ya tofar da miyau

Alhaji ghali yai murmushi kingama madam Tai murmushi na Gama yallabai na ya Kara chacumo shi sai shewa Nan nauwara zuciya debe ta ta mike Kai alhaji ghali Dan akuya Dan bunsuru tunda nake ban taba ganin Dan iskan namiji irin kaba Allah yai wadaranku shaidanu kawai Kuma zaluncin dakai mun sai Allah ya saka mun mugu azzalumi macucu Bata Gama rufe Baki ba ta Fara Jin saukar duka ta ko Ina wani naushi da akai Mata ne yasa ta zube warwas a sume ba Wanda yabi takanta suka Gama shakiyan cinsu akai addu'oi suka ajiyewa baby Chakwai abunda suka kawo na siyan Baki suka fita anata iskanci kaci ta a hankali alhaji ghali karka yi Mata illa Dan naga rawar Kai kake

_To fans maji magani Allah ya tsaremu ya tsare imanin mu Wanda ya Bata Sai dai addu'a nice

Taku a Koda yaushe_

*Feedyn bash*
[11/13, 7:13 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *🧑‍🎓DAN ISKAN NAMIJI🧑‍🎓*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

_*Assalamu alaikum' my fans' Dan Allah kuyi min uziri kwana biyu bazaku dinga samun typing me yawa ba' saboda wasu dalilai ,amma indai komai yai settle insha Allah zan dinga muku da Dan dama, nagode sosai masoyana.*_

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DA SUNAN ALLAH ME RAHMA ME JIN KAI*

55-56
```

Hajiya Ameera santalous  direct gida takai lawan,ta kalle shi "lawan ya kamata ka nutsu dan Allah banji dadin abunda ya faru ba Ina so kayi tunani a kaina aure nakeso miyi"shiru yayi Yana kallonta dan abun yaji wani iri shi Ina ze kai Mata "nagode hajiya insha Allah zanyi tunani akan ki,zaki ji amsa nagode da kokarin ki akai na" ba wanda ya kara magana ya bude kofa ya shige gida,girgiza kai tai kawai "tunda na ganka nafara sanka bana neman Abu na rasa a rayuwa komai wahalarsa"taja mota tai gaba

Dare ya tsala sosai ya shiga gidansa,"ummi ke ke dallah fito ki ban abinci yunwa nake ji,yadinga buga Mata kofa a fusace ta fito "wai lafiya? Koko yau iskanci naka a kaina zaka sauke shi?da chan kana cin abinci a wajena ne koko sabon iskanci ne to ban da shi mun cinye, kan uban nan Kai"kin isa ki hanani abinci a gidana to wallahi ko kiban ko jikin ki ya gaya Miki yanzun nan!mtsww "baka da hankali ne koko giyar taka ce ta gayama karya to rabon da ka kawon kwayar shinkafa Kai kanka ka manta Dan haka kanka akeji"da sauri tasaka sakata, habawa zuciyarsa ta sosu ransa ya gama baci.

Wallahi baki Isa ki bacci ba baki ban naci abinci ba!Nan ya dinga buge buge ya hanata bacci dama da wuta karshe ya Dakko radio dinsa ya jonata, ba ita ba har makota sun kasa bacci' Yara duk sun tashi amma taki budewa dan tasan wallahi da ta bude sai dai Allah,Dan sai ya zane ta a Daren nan yai watandar ta, dake ya saba kwana jin kida shi be dame shi ba Haka ya wuce dakin sa ya kwanta ya dinga bacci. cikin ikon Allah nna idar da sallah nepa suka dauke wuta,sannan suka samu suka rintsa yaran gashi akwai school cikin sanda ta zare sakatar dakin nata.

Ta dakko risho da kayan girki ranar a daki ta hada musu abincin Kari ta zuba musu na lunch boxes, lokaci nayi ta kwashe su suka fice yana ta sharar bacci sai goma ya tashi jiyai duk duniya ba abunda yakeso irin doctor saudat, shi tuni ya manta da wani abu da ummi tai masa, cikin sauri sauri ya shirya ya dakko wayarsa ya Kira abokinsa Wanda suke wa lakabi da milloniya" ya baba ina motata" ai "tun jiya na dauke ma ita tana gidana ga Kuma sabuwar da kaci kirar Honda Accord" hehehe !yai wata shu'umar dariya "ganinan zuwa yanzu" Kai tsaye gidan milloniya yaje be wani ja zance ba ya Karbi key sai gidan saudat.

Yana zuwa yai horn aka bude Masa, ita ko tun da taji horn tasan aikin su yaci Dole ta auri lawan ta fanshe abun da yai Mata wallahi sai ta takura rayuwar sa sai yayi nadama da Dana sanin auren, shiru gashi bashi da number din ta' ya nemi alfarmar me gadin yai Mata magana. Yana Gaya Mata tace a shigo da shi suka shiga yana zama ta mike a fusace "me kazo yimun a gida ko Nan ma kabiyo Ni ka wulakanta Ni Dan nace Inasan ka" jikin sa yai sanyi ga wani mugun Santa daya ke naji "nayi kuskure kiyi hakuri".

Hmmm! "to shikenan zauna" yanemi guri ya zauna lawan! $wallahi"Banda Inasan ka sai kayi nadamar sanina a rayuwarka ko a tarihi ban taba ji ko ganin Dan iskan namiji irin kaba matar ka ta sunna ka bita har gadon asibiti saboda Dan akuyane Kai hakan bema ba sai da ka bi likitar ka keta Mata haddi Amma Kuma silar hakan naji ba Wanda nake so sai Kai zan aure ka nasan Kai ma auren nawa kakeso Amma kasani bazan dauki iskanci ba" ita duk tana haka ne Dan ta gwada taga aikin nata yayi, mmma batansan cewa kwabar ta tai ruwa ba. Bata Ankara ba taji ya Wanka Mata Mari idonsa jajir "banzo Dan ki wulakantani ba!

"Nazo ne akaran kaina Dan Inasan ki zan aure ki Ina jure komai Banda iskancin mace ki kiyaye kisan dawa Zaki zauna, kuma aure tunda kin nema za'ayi shi karki damu tunda iyayen ki suna fushi dake kije ki nemi gafarar su, Amma ki sanar dasu Dan iska dai dai dake Kika samo, Wanda karyane matarsa taci amanarsa idan ya aure ta tunda duk takun ta a tafin hannunsa take. hawaye doctor saudat kawai take "Kuma kika kuskura Kika kara yimun banzar magana wallahi sai jikin ki ya Gaya Miki ya manna glass din sa ya fice"

Dora hannu Tai ta dinga zunduma ihu "wayyo Allah na lawan ka cuceni" nan da nan ta Kira kawarta "kawata akwai matsala lawan yazo yaci mutuncina harda gorin Ina neman wani da aurena" ke "mekikai masada har ya gaya Miki Haka" Nan ta kwashe komai ta Gaya mata, "gaskiya saudat Baki da hankali kinman ta abunda malam yace sai a hankali ke Kuma sai ki zake kisan yadda Zaki shawo kansa" hanya dayace nayi dabarar daukar number dinsa a wayar Laila matarsa, ok "hakan Zaki Naga taji sauki wallahi tausayi take ban yau za'a sallame ta.

Da kyar arfan ya samu Tai shiru, ya dauke ta chanchakat ya Kai ta bandaki ya Tara zuwan zafi a baf yasa ta a ciki, minti goma ya cireta ya sa wani me dalan dalan sai kuka take, jiyake kamar ya maida ta ciki kamar ya rungumeta. da kyar ya barta Tai wanka shima yaje yai wanka, tana fitowa taga missed call din ta bita "umman tace kina inane gamu a asibitin"umm "naje dafowa anty abinci ne gani Nan" a'a "kema Baki da lafiya ne naji muryarki wata iri" lafiya ta kalau mura nake danyi na kuma yi dan bacci ne. to sai kun karaso taka she kiran, tasaka abaya ta yane fuskar ta da mayafin tayi kyau kamar balarabiya ta fito parlour dakyar take tafiya.

Ta tarar da arfan yayi wanka yasha kana Nan Kaya, "baby ki zauna a gida kinji zance Baki da lafiya" ta balla masa harara "Hala Baka da hankali ne" ya zaro ido, "nine bani da hankali" hhhhhh! ta sheke da dariya,sai ta Kara burgeshi Tai Masa kyau, yadinga yi Mata hotuna Bata sani ba, sai da ta gaji Dan kanta ta kalleshi, fuska a hade "kayi tunanin kana da hankali ne? ai baka da maraba da Wanda yake turu, ka nemi Yaya kanemi kanwar ta, wallahi arfan Kayi asara yadda ka tarwatsa rayuwata Allah ya tarwatsa taka duk .."be bari ta karasa ba ya rufe Mata baki, hannun ta kawai ya Kama tana ta kuka yaja ta har waje ya sata a mota.

_To fans, kuyi manage da wannan wallahi typing akwai wahala, sai a slow,nice taku a kullum a koda yaushe._

*Feedyn bash*
[11/14, 9:18 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *👳DAN ISKAN NAMIJI👳*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*WANNAN PAGE DIN, NAKU NE MALAMAI NA MASU SAN CI GABANA.*

*Malam Almu Dakata*
*Malam Yusuf Gumeil*
*Malama Black Girl*

_*Nagode sosai da yadda kuka tsaya mun tsayin daka wajen ganin ci gabana, gashi a kwana biyu har wasu nake ko yawa yadda za su tafi da lamarin su na rubutu. duk da ban gama kware wa ba, amma alhamdulillah! nagodewa Allah, nagode muku, Allah ya biyaku da gidan aljanna.Dalibar ku me kaunar ku Feedyn Bash*

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

57-58

Tuki kawai yake Amma bema San Ina yake sa gabansa ba.Gaba daya hankalinsa a tashe yake baya san kukan ta, parking yai a gefen hanya ganin idan be tsaya ba to lallai ze iya hada accident a hanya, hada hai yai da sityari yai shiru kawai shi yasan zugin da zuciyar sa ke masa, ba shiri ya dago da kansa, ya jawo ta jikin sa, beyi aune ba jiyai ta waska masa mari."Angaya ma dan na kyale ka hakan na nufin zakaci gaba da yin duk iskan cin da kake so dani.Wallahi kayi kadan". Dafe kuncin sa yayi yana murmushi, "bazaki taba batan rai ba, dan sanki nake har
```

jinin jikina". mtsw! ta tofa Masa yawu a fuska, ya shafo yawun ya lashe yaja motar Yana murmushi suka Isa asibitin.

A fusace ta bude motar. Ta fuce ta bar shi,sai shiya dakko plask din farfesun kazar, Dan Yama manta Dana dankalin sai yanzu, jiki a sanyaye ya shige shima. Tana shiga taci Karo da umman ta da Mama duk suna asibitin, "ke Kuma sai yanzu"?cewar umma, karaf taji ya shararo karya, "umma nadan fitane ba dankali a gidan naje siyowa, sai Kuma akai min waya inada Baki a office, shiyasa na dade. "Amma ayi hakuri ba lefin ta bane lefi nane, kafin na dawo har ta gama farfesun ba'a samu dankalin ba".

Murmushi mom dinsa tayi, "wani dankali har naje gida nayo Mata, gashi Nan ma tana ci". Daddy ne zaune a gefe' sam baya fuskantar mema suke cewa, ya nutsa cikin tunani. Kenan dama kanwar nafeesat ce matar dansa? innalillahi wainna ilaihirrji'un, zufa ce take ta keto Masa ba Wanda ya kula da halin daya ke ciki, wannan wane irin tashin hankali ne haka? "tayaya zasu fuskance ni? nasan Allah be Haram ta mun ba,amma ana barin halak ko dan kunya,gaba daya tunanina na dauka Yar aiki ce, nasan abun zezo mun da sauki, ashe abun babba ne, hmm!.

Dan har ya gama plan din ta koma gidan su,a zuwan ta dena aiki.Baze gaya musu ita ze auro ba, sai dai su ganta. Ashe abun babba ne, amma ya mikawa Allah lamarin sa,ze dage da gaya Masa, yasan baya bacci idan da alkhairi a lamarin Allah ya tabbatar, idan Kuma babu Allah ya cire masa ita a ransa. "alhaji alhaji lafiya ina ta magana," na'am na'am "ya aka yi hajiya" ina ta magana yau she zaka tafi,tun da sun dawo kace kanada uzuri."eh yanzu zan tafi idan kinji ni shiru ki Kira driver ya dauko ki" ya ajiyewa su mama kudi ya fice, ba Wanda ya gane halin dayake ciki.

Ango Bello sun shigo shi da abonkan sa, sun tarar da amarya ita kadai tayi kyau no ban mamaki. Ta sha kunshin ta kafa da hannu sai walwali take, tana zaune a parlour kai kace parlour din diyar wani hamshakin ce,su kansu a ransu addu'a suke Allah ya basu mace kamar maimunatu.Suna shigowa ta sakko kasa saboda ladabi, ba yadda basi ba amma taki komawa saman kujera. Nan suka zauna babban abokinsa sani ya dinga yi musu nasiha, "kuyi hakuri

zaman aure Dan hakuri ne' kuji kuki ji, ku gani ku ki gani, duk marayu ne ku ku rike maraicin ku, kurike ubangijin ku, sai ya dafa Muku, Allah yai wa auren ku albarka ya kawo zuri'a dayyiba saliha. "Ameen" suka amsa gaba daya.

Suka danyi hira yawanci duk tunasarwa ce da addu'oi, suka mike suka ajiye abunda suka riko musu da alkawarin gobe zasu kawo ragowar kayan.Bayan ya rakasu ya dawo,ya rufe gidan ya shiga kitchen ya dakko plate da kofuna,ya fito ya shiga dakin nasu ya bude ledar kajin, kunshi biyu ne, daya guda biyu ce sai daya guda daya, ya dauki me guda dayar ya hada fresh milk guda daya, ya kaiwa Inna.Dake ba kowa sai ita daya tun da ba dangi ne da ita ba, har ta Fara bacci ya tashe ta ya bata kazar da fresh milk din,habawa Inna nan ta far musu daci to an dade ba'a hadu ba,ci ta ke tana sa musu albarka,sai da yaga ta koshi ta ture dan kan ta,sannan ya gyara mata kwanciya, yai mata sallama ya rufo dakin ya koma dakin su.

Har ta gyare wajen ta kwashe kayan tea din ta sasu a kitchen.Ta juye kazar a plate, ta dora a kan center table, tayo alwala tana nafila saboda Sha biyu tayi. Yana bude dakin wani kamshi ya dake shi, alhamdulillah! ya fada sannan ya shiga yaga bata parlour,daya shiga uwar dakin ya tarar tana sallah, sai shi ma ya dauro alwala ya dawo ya jira ta ta sallame, kanta a kasa "kin idar" tace "eh". "To tashi maza miyi nafila mu godewa ubangiji da wannan baiwa da yai mana." maimunatu! Ya kira sunan ta "ke alheri ce a gareni. sanadin auren ki Allah kadai yasan alherin dana samu."Murmushi tayi ba ta ce komai ba, ta mike tsaye kawai, yaja sukai sallah suka idar,ya kama goshin ta ya din ga kwararo mata addu'oi. Bayan ya gama yai mata tambayoyi akan addini, duk ta amsa ba inda ya samu wata matsala da ita, yaji dadi har ransa.

Maimunatu! ya fada da wata iri Yar murya da gaba daya tsigar jikin ta sai da ta tashi.Ina so kiyi hakuri dani dan Allah! ki so ni ki kaunace ni, banda kowa a duniya a yanzu, daga ke sai Inna ta, baba na me kauna ta na rasa shi tun ban gama mallakar hankali na ba. Inna ta ci gaba da daukar dawainiya ta, karshe lalura ta sata a gaba.Ina ji Ina gani banda kudin Kai ta asibiti, komai na kudi ne a wannan lokacin, kiyi hakuri da duk halin da zamu kasance ki kula mun da mahaifiyata. Banda kowa sai ita, dan Allah maimuna! zanyi kokari zan sauke duk nauyin ku daya rataya a wuya na.

Murmushi tayi! "mijina ne Kai, aljanna ta, in dai inasan ka saboda Allah to zan so mahaifiyar ka. Saboda haka ka kwantar da hankalin ka, ina da sana'a wadda zamu hadu mu rufawa kan mu asiri, Allah shi ne me yi, waya San me gobe zata haifar, ina fatan Allah ya bani ikon yi ma biyayya kai da inna".Besan san da ya rungume ta ba, saboda dadi chak ya dauke ta sai parlour, ya cika mata cikin ta tun tana noke wa har ta saki jiki, yaci shi ma ya koshi, ya dauke ta chan cha kat sai gado, yana shiga ya kashe fitilar dakin dakin yai dun dum.

_Asuba ta gari amarya da ango, asha love lafiya a Kara hakuri dani,nice taku a kullum a Koda yaushe_

*Feedyn bash*
[11/16, 9:18 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *💆🏻‍♂️DAN ISKAN NAMIJI💆🏻‍♂️*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

59_60
```

Da asuba ya tashe ta, abun tausayi ta wahala iya wahala shi ko sai murna yake. Ita ko kunya take ji yadda ya dinga kuka yana ihu, tsoro ta dinga ji kar inna ta jiyo, ta dinga toshe masa baki, amma ina daya sa kai ita kanta sai ihu. Bata kara sanin inda kanta yake ba sai yanzu,dan azaba ce tasa ta bacci, hankalin sa yayi kanta "ki daure kona daukeki", ta girgiza kai ya kama hannunta ta saki uban wani ihu.Cak ya dauke ta sai bandaki, dama ya cika baho da ruwan zafi ya sata a ciki, ta kara sakin wani ihun. "kiyi hakuri dan Allah! ki daure kar Inna taji", ita wallahi tama manta da wata inna a gidan.Ya tsaya yai mata wanka tai wankan tsarki, suka koma daki sai yaji kira a masallaci, da sauri yace "Maimunatu bari inje karna makara, idan nadawo na gyara Inna, yau na makara sosai"ya wuce be jira cewar ta ba.

Mikewa tai ta saka kayan ta tai raka'a tanul fijr, tunda ba a kira assalatu ba, ta fito duk da tana jin radadi haka ta daure taje ta tarar Inna ta farka, amma ba kafa tana zaune ta dai yi fitsari a fo. Da sauri ta karaso, "sannu Inna! cike da tsantsar tausayin rashin diya mace. Suka gaisa, bari ina zuwa yanzu, ta fita hada ruwan wanka me dumi, dake suna da wuta dama,tana da buta kuma Bello ya dafa ruwa. Ta dawo ta kamata ta daga ta, ta kai ta bayi, tana "bar shi kiji da kanki" amma ina haka takai ta ta tsaya tai wanka ta dinga zuba mata ruwa tana alwala. Suka gama ana tada sallah a masallaci, tai sauri taba ta zani da hijab ta sanja, ta dauki wani hijab din suka bi jam'i .

Suka idar da sallah, inna sai sa mata albarka ta ke, taji dadi a ranta nan ta sanja mata kaya masu kyau, suka zauna suna dan taba hira duk da Maimuna kunya ta rufe ta," dan Allah y'ata ki dena jin kunya ta na daukeki tamkar Bello, idan kina suruka dani bazan ji dadi ba, ki sani sahun mahaifiya kinji." Ta daga kai insha Allah.Sai ga Bello cike da sallama ya shigo, turus yayi ganin inna shar da ita har tayi sallah. "A'a inna waya gyara ki haka," Tai murmushi! "diyata mana har munyi sallah wallahi naji dadi Bello, karike Maimunatu amana ko bayan rai na, ina so karike malam baka da wani uba a duniya sai shi. Jikina na bani zaka zama wani abu a duniya, ina yawan mafarkin hakan, karka kuskura ka wulakanta Maimuna, ka kyauta tawa malam." Nasiha me shiga jiki ta dinga yi masa me kamar wasiyya.

Maimuna kwalla ta dauke na tausayin wannan tsohuwar shi ko Bello dan dai jarumi ne jikin sa yai sanyi kalau haka taci gaba dayi musu nasiha da hakuri da zaman duniya da rayuwa kuje ku kwanta Allah yai muku albarka akwai gajiyar biki a tattare daku haba inna abinci zan dora me zaki ci murmushi ta saki wallahi diya ta alhamdulillah kinga ga ragowar kaza da wannan abun

sun ishe ni bari in kawo miki ragowar tamu kai wane mutum wannan din ma tai mun yawa da ta bude tafi rabi da kyar suka yarda sukai mata sallama suka wuce dakin su yadda Bello ke nani kar ta shine abun da ya daga mata hankali idonta yai rau rau zatai kuka

Dariya ta bashi amma ya dake meye kuma dan Allah kayi hakuri hhhhhhhh wallahi kin ban dariya bazan miki komai ba abu daya ne ki temaka mun ki barni na tsotse ki san rai na dan Allah karki hanani rufe fuska tayi cike da kunya ustaz ba kunya ga iya love nan ya cire mata kaya tas ya tike ta shi ma ya taki nan zance ya sauya salo dif ya kashe fitila baka jin komai sai gurnanin ustaz Bello wani irin nishi Maimuna take wayyo akeena kiyi hakuri ukti abun da kawai nake iya ji kenan

Karfe tara aka fara buga musu kofa Bello ne ya taso idonsa taf da bacci takaici ya gama cika shi waye ze shiga rayuwar su Allah yasa ba yan uwan amarya bane yana zare sakata yaga walid kanin Maimuna rike da wani uban kwando ya tsuguna har kasa ya gaida shi ya amsa gashi inji umma to madallah kace mungode anty rahila tace bayan azahar zasu zo baza su zo da wuri ba saboda aiki yai musu yawa ba karamin dadi yaji ba dan dama yayi ta'asa a ciki yace baze ba amma dakanta ta yarda yayi amma ta tubure masa da kyar tai bacci ya karba ya koma daki ya bude farfesu ne nakan rago yaji kayan kamshi sai funkaso da miya sai ruwan shayi daya ji kayan kamshi ya dakko plask ya dibawa Inna da kyar ta karba

Sai sha biyu suka tashi ya kamata tai wanka suka shirya taji dadin farfesun a cooler yake da zafin sa haka ta dinga ci tana shan romo karfe daya yai mata sallama ta raka shi ya fita ta koma dakin inna ta tarar tana bacci ta koma nata dakin ta dakko littafin ta na addu'oi tana karantawa wajen biyu sai ga kawayen ta nan suka baza haja aka dinga hira sai bayan azahar sai ga uban abinci daga gidan su dama suna Shirin dorawa sai da ta dibi na mijin ta ta ajiye ta zubawa Inna sannan suka diba nan suka dinga hira har wajen hudu sai ga kannen umman ta

Ba kowa a parlour din sai ita dan ta doku a wajen abokan nasa ne bayan sun fita alhaji hassan yace gaskiya abun da mukai be kamata ba dokar da baby chakwai tasawa matar alhaji ghali yayi yawa meyasa yasan baya santa ze aure ta be kamata ba gaba dayan mu bama san gaskiya ina wannan sabgar amma wallahi ko bana so ina kyauta tawa matata habawa sai alhaji

tsula ya fara bala'i wakake nufi baya kyauta tawa tasa matar wallahi ka fita ido na dama ina da da cikin ka wallahi yanzu zan haifeka nan aka fara bashi hakuri amma kamar tura shi suke gashi suna gudun kar makota suji abunda suke gudu ya afku.

ransa ya baci abin nan fa ba dole bane sa kai ne ba Allah ne yace miyi ba mu muka ga dama muke yi wanda Allah ma yace miyi takewa muke bamayi kuma da kake tada jijiyar wuya tsarguwa kai kasan bakayi ne banda rainin wayo na kama suna ne bare kace nan aka shiga tsakani idan ka isa kace daga yau ka dena ai gaba dayan mu neman duniyar muke waye be same ta ba dan rainin wayo kawai yadin ga zaginsa da kyar suka samu yaja motarsa yai gaba ina rokon Allah a koda yaushe ya yanke mun wannan wahalar banaso na mutu ina aikata wannan sabon.

Nan suka bashi hakuri, suka tambaye shi meye shawara.Shawara daya ce,mu koma mu gyara kuskuren mu.sun yi na'am da maganar sa suka kira alhaji ghali wanda har sunyi shirin bacci shi da amaryar sa sukace zasu dawo zasi magana yace to amma ransa be so ba suka koma tana kwance sukayi musu fada akan abun da ya faru inda baby chakwai ya buga tsallen albarka yace bazata sabu ba bindiga a ruwa yai zaman kishi sai dai wallahi auren ya mutu ba shiri alhaji ghali ya fatattake su yace bakin ciki suke masa suka fice ransu ba dadi duk a jagule da hanzari ya saka sakata

Ya dakko ruwa me sanyi ya tsiyayawa nauwara wanda a firgice ta mike ya danko ta wallahi wallahi wallahi kinji nai miki rantsuwa uku kika kuskura kika gayawa wani ko wata inada wata matar bayan ke ko kice nayi auren jinsi ina zuwa baby chakwai yaja dogon tsaki ai wallahi duk wadda ta hada kishi dani ta janyowa kanta bala'i sai ga alhaji ghali da bindiga a hannu kingan ta wallahi dai na harbe ki na kashe ki na kashe banza na karar da duk dangin ki jikin ta na rawa wallahi bazan fada ba nayi alkawari amma kai mun alfarma gobe akwai budar kai daza'ai anan gidan kan uban nan wallahi kinyi kadan cewar Baby Chakwai daga gobe da asuba aikin ki ze fara nagaya miki

_Gaskiya fans magana ta gaskiya comment yayi sanyi sai ku karanta kuyi shiru idan kuma kungaji da book din ne kugaya min Dan wallahi ni kaina idona ya fara ciwo saboda typing nice Taku a kullum a koda yaushe_

*Feedyn Bash*
[11/17, 9:11 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *💆DAN ISKAN NAMIJI💆*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Wannan page din sadaukarwane agareka Hassan ATK. Nagode sosai da yadda kake mun posting a Facebook, Allah yabar zumunci.*

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

61-62
```

"Wallahi kika makara na lahira sai ya fiki jin dadi. kuma ban lamunce kowa ce mace tazo gidan nan ba,saboda haka ma zan kawo sojoji gobe su fara gadi,wanda suka ga ze musu hauka su harbe shi".Ido ta zaro! eh "kuma gobe ki tabbatar in kin gama aikin ki,karki fito dan a goben zami party na murnar aure na. Kinsan bami a Nigeria ba, saboda yan sa ido, amma gobe karfe hudu zamu fara, kini dokoki na ki zauna lafiya.Koba haka ba alhajina?"yai wani farr da ido, "wannan haka yake zaman lafiyar ki kibi umarnin amarya ta, masoyi yata, baby chakwai, ba rashin ci da sha,komai za'a kawo miki amma ki kiyaye."

Idanunta na zubar da hawaye,"naji insha Allah zan bi" ya wani kwabe fuska "naji maza ki tashi ki wuce dakin ki, nai miki wannan alfarmar, tunda baki ja dani ba, kai kuma Alhaji muje daki.Jikinsa har rawa yake, ya wani rungume shi, wayyo dadina.Galala nauwara tayi kawai, dan abun yafi karfin tunanin ta, nan taga ba kunya sun fara shafar juna suna tsotsen juna. Da hanzari ta wuce dakin ta tana ta kuka kamar ranta ze fita, tana shiga tasa key ta fada gado tana ta zunduma uban ihu, kamar ance uwarta da ubanta sun mutu, bacci dai bega idanun nauwara ba, duk da ance barawo ne, gaba daya kwakwalwar ta tadau chaji.Dama da gaske maza na neman maza? abun da yake daga mata hankali kenan, ga barazanar da akai mata.

Da duku duku ta tashi ta fara aikin ta, Allah ya sota gidan ba kura sai wani uban girma, tana aikin tana kuka wiwi, ga gajiyar biki ga rashin bacci, tana ji tana gani ta share ko ina ta bawa flower ruwa ,saukin ta daya akwai mesa. Karfe takwas ta gama, har ta zauna ta tuna da girki jikin ta na rawa ta mike ta fara kiciniyar dora girki, bata iya abinci sosai ba, ta tuna tana da littafin girke girke, da hanzari ta dakko ta fara daukan masu kyau, dan ita harga Allah tsoron mijinta take, da wannan katon banzan me suffar rashin imani. Nan ta har hada kadaran kada han, gashi nan dai kala uku tai, daya magi yai yawa, daya yai bala'in shan mai, dayan ko duk ya jagale.

Ta zuba a warmers. Ta dauke su takai kan dining. Tana ta murmushi tasan dole zata burge alhaji ghali, dan wallahi bazatai sake da wannan daular ba, jikin ta a mace dan ta aikatu, tayi masifar gajiya, ta wuce dakin ta. Tai wanka tana fitowa ta kira meena, suka gaisa "ya komai ya kammala" uhmm! "a'a meena baya jin dadi ne,ga gajiya yama hana budar kai din dazami, yace bayaso ya hana kowa ma zuwa,"ita kanta bata san sanda take shararo wannan karyar ba. Chab nauwara baze yiwu ba, baki da hankali ne, yadda kawayen mu suka ci buri, wallahi baze yiwu ba ta katse wayar.

Tana zaune ta hawaye taga an turo kofar, har ta zabura ta mike ,taga alhaji ghali yana sanda. "Nauwara kiyi hakuri da batun budar kan nan, amma tunda kina so nasa akama miki hall me kyau, kuje kuyi amma karki gayawa baby na, nina hada miki, kawai ki tambaye ta zaki fita a zuwan dubo umman ki, tunda tasan bata da lafiya." wuf ya fice kuka ta saka wiwi ,yanzu nida mijina sai dai labe kuma akan namiji, ya Allah ka dawo da Alhaji Ghali tafarki na gaskiya, Allah na tuba nima ka yafemun, wallahi ba inda zani na fasa, gwara naga wainar da zaku toya a gidan yau.

Alhaji malle be taba nadama da dana sanin iskanci da zina ba sai yau. Ba abunda yakai zina tozarci da zubar da mutunci, safiyar ranar zance ya watsu a gari. Gashi human rights sun shiga cikin lamarin, abu ya kara kwabe wa, dan sun tsayawa yarinyar ancire masa uniform yana ji yana gani, duk da haka anso a sake shi tunda an kore shi daga aiki. Amma human rights sun tsaya kai da fata sai sun karbar wa yarinya hakkin ta sun shigar da magana kotu, ranar alhamis za'a fara zaman kotun.

Dr Saudat ta sallami Laila, taba shawarwari yadda zata kula da kanta  Tai mata godiya, suka wuce gida da gwaggo. Sukai waya da lawan yazo, nan ya bata hakuri akan abun da ya faru, tai masa iso wajen baffan ta ya bashi hakuri, da alkawarin baze kara ba, yace shi ba ruwansa, yarinya taji ta gani to falillahil hamd, ya bashi wata biyu yasan inda ze sata, ya dauke ta daga gidan. Ya yadda akan hakan, sun dade suna hira kamar wani abu be taba faruwa a tsakanin su ba. Ta dakko masa albashin ta, dake anyi salary, akan yai gyaran gida,yace ba komai ya gode ,ya bata dubu biyar a ciki yasa a aljihu sukai sallama ya tafi.

Kano club yaje inda suke haduwa dukan su. Nan aka fara ihu ana sowa, sai dan iskan namiji maganin shegun mata. Manya manya maganin kana nan kwari, "yarinyar nan fa ta warke, amma tana asibiti tana shan alwashi akan ganin bayan ka". Hhhhhhhh! Haba dan Allah? Wallahi "kasan karfa ce bata da mutunci, cewar miloniya hhhhhhhh! "wallahi kaban dariya, uban masu kudi, karka manta da lawan take magana, manta da wannan banzar.Ya ina daya motar tawa," "tana gidana" "kwalar da ita zanyi saboda zanyi gyaran sama na. Zansa Laila achan, anban wata biyu kuma inasan yarinyar, da nadauka guzar nakewa, ashe akwai ta a raina." Suka dinga dariya boss yace yana so ze siya. Lawan ya banka masa harara, "bata sata bace kasan" aka kwashe da dariya! ai min sani babaa, serious, shikenan zami maganar.

Niko lawan na tambaye ka?cewar miloniya "ina jinka",hmmmm! "wai ya akai ka tonawa mande asiri, be kamata ba lawan.Zaman tare bece haka ba."hhhhhhhh! wallahi kaban wata muguwar dariya."mande haramci ya gwada mun irin nasu na Yan sanda"."amma duk da haka,lawan be kamata ba",kaga "wallahi tunda ya nunan ba amana, ba sani ba sabo, dole nima inuna masa nawa iskancin yafi nasa.koda kisa nai yaci ace mande ya tsaya mun. saboda abotarmu, amma karshe tura ni norman sland yai, kaga karshe gani ga kotu, inma kashe ni za'ai a kashe, shi bashi da matsala ya manta nasan sirrin sa, shiyasa na fasa kwai."suna cikin maganar aka kara karuwa, aka share zancen.

An shiga kotu da alhaji mande da human rights. inda aka fafata ,aka yanke masa hukuncin shekara biyu a gidan kaso, da tara me yawa saboda lalatawa yarinyar rayuwa da yai, tace shi kadai ke neman ta. anyi duk text din daza'ai ance normal, amma abun tsautsayi tana da ciki karami,inda alkali ya yanke hukunci bisa rokon human rights, akan idan yarinya ta haihu za'a daura auren su da Alhaji malle.beso wannan hukuncin ba, babban tashin hankalinsa karin auren da akace zeyi,yazeyi da matarsa yar bala'i,data tsani kishiya a rayuwarta,haka shari'a ta tashi aka iza keyarsa zuwa gidan kaso.

Lawan da doctor saudat sun shirya  soyayyace suke yi ta sirri, yace besan kowa yasani, itama a nata bangaren haka, haka suke Shan love dinsu hankali kwance, amma yace aure ba yanzu ba gaskiya. yana da wata ma basu tare ba, kuma ta sani, amma yai mata alkawari da sun tare ba dadewa ze aure ta.Hajiya Ameera tayi tafiya, shi yasa koya Kira wayar ta baya samu. Yaji haushi dabe san gidan taba.Sai yau ta kira take ce masa taje saudiyya, kiran gaggawa ne ya same ta,amma karya manta da maganar auren su.Hankalin sa ya tashi yazeyi,ga saudat ga hajiya Ameera santalous, da wacce zeji?gaba daya ya shiga tunani, kowacce so yake, kuma kowacce akwai ta ga yayan banki.

*TO FANS SAI NAJI COMMENT DINKU NAGODE SOSAI DA KAUNARKU AGARENI*

*FEEDYN BASH*
[11/26, 6:43 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *👨🏻‍🔬DAN ISKAN NAMIJI👨🏻‍🔬*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*~Assalamu alaikum my fans Kuyi hakuri bisa tsaikon da kuka ji na shiru kwana biyu kuyi hakuri wallahi Banda lafiya kullum muna zaryar asibiti shiyasa kuka jini shiru wayanda suka sani suke ta yimun addu'oi nagode Allah yabar zuminci musamman kainuwa writers, feedyn bash real fans1&2.nagode sosai da addu'oin ku da kulawa Amma bazan dinga typin kullum ba gaskiya nagode~*

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

63-64

Lawan ya samu ya gyarawa Laila benan gidansa duk da kullum a bala'i suke gida ba sauki waje ba sauki haka ya zage kowacce yake nadar ta dan yace basu isa su daga masa hankali ba akan menene wallahi aure yanzu ya fara yinsa wadda bazata zauna ba cikin su to ta kara gaba gefe guda hajiya tana hanyar dawowa daga Saudi inda ta dagawa Lawan hankali akan
```

maganar auren su ta sakar masa bakin aljihu kuma tace a gidan sa zata zauna ita bazata zauna a gidan ta ba saboda aure tayi ba zaman kanta ba  tace bata bukatar komai ita zatai sadaki kawai ze nema

Yau take ranar kai amarya abokan lawan sun masa kara motoci dai masha Allah sun hadu luntsuma luntsuma sunyi jeran gwano amarya tai kyau masha Allah dama Laila ba karya akwai kyau ba wani taro tai ba yini ne kawai tayi shi angama za'a tafi kai amarya nan suka din guma sai mazauna Masha Allah gidan Lawan yayi kyau yasha fenti milimil abinsa nan yan Kai amarya suka fara  shiga suna hawa sama masha Allah ciki da parlour da karamin daki da bandaki da kitchen din ta komai nata normal

Har sun hau sama da ita sai kaka karta tace be kamata ba akaiwa uwargida ita amana suka sakko suka shiga da ita dakin sukai sallama ta amsa musu tana zaune tana kada kafa kamar gaske da kawayenta su biyu suna hira aka gaisa kadaran ka da han nan kakar Laila ta fara magana to Yar nan ummi ko kiyi hakuri da Yar uwarki ku zauna lafiya aure ne ya hadaku Dan Allah kuzauna lafiya Kinga kece babba kija girmanki ke kuma yi nayi bari na bari bansanki da rigima ba Laila dan Allah ku zama yan uwan juna kuzauna lafiya

Hehehehe suka sheke da dariya kai iya kinada kinibibi inji kawar ummi meya hada kishi da yan uwantaka idan kanwar tace bazata yarda ta auri mijinta si zaman aure ba sai dai idan mutuwa tai ya zama dole to a wane nassin ma akace kanwarka ta auri mijinka indai ba aure kukai ba banasan kinibibi kun kawo mata kishiya suyi zaman kishi maganar Yan uwan taka Babu kowa yaji da kansa dan Allah kuja tsumman rayuwar ku kuyi gaba mtswww inji dayar kishiya ko masifa
abunda munada tarihin yadda akai auren wace tabara ce basi ba ita da shi a waje ai wallahi ba mutunci dai zuwa munsan komai

Ran kanwar babanta ya baci ya isheku haka wulakancin ya isa kune Yan hana ruwa gudu munafikai baza kuyi musu fatan alkhairi ba sai na tsiya munafikai daga ganin ku zawarawa ne shiyasa kuke bakin ciki dan tayi aure ku zugata ku rusa musu auren dan kunfi kowa sanin cewa mijinsu yafi ku iya iskanci idan kuna ganin in kun zugata riba zakuci ke dakata ke Kuma awa

ummi ta mike nice Nan nasasu saboda banasan wahala amma tunda kunnema zan nuna muku kalata yanzun kakar Laila gyara zama tai ta gwalo ido tana ganin ikon Allah

Kun kawo yarku gidan mutuwar ta makabar tarta dan wallahi bazan kaffara ba sai naga bayan ta shegiya Yar iska yar giya mazinaciya wallahi baki Isa ki zauna a gidana ba wallahi tuni Laila ta mike a fusace ki kiyayeni dan banida mutunci ta lailayo wani ashar ta narkawa ummi nizaki cewa nasha giya yau zan nuna miki aikin yan giya nida mijin naki da kike takama tare muke iskancin muna Shan giyar nan ummi ta hango wata kwalbar lemo kafin su ankara ta rotsawa ummi ta saki ihu tace ku dakkon kayan aiki suma da Shirin su

Suka fada uwar dakin ta sai ga Mata na fitowa suka rufe su da duka suka hau har sama suka Fara operation suna jibgar yan Kai amarya batai wata wata ba ta dakko wata kwalba Ashe acid ne tayi kan Laila dake kiciniyar daga yagwalgwal kakarta Allah ya temaka ta kautar da fuskar ta ta shara musu ya sauka a kafadar ta da gefen hannun ta ya zuba a kafar yagwalgwal lokaci daya suka saki wani uban ihu

Suka zube gida ya hautsine da ihu hankali ya tashi banda kuka ba abunda ake mata sai fita suke da gudu sun mata raga raga da kaya nan da nan aka Kira lawan abokan sa suka kawo dauki Amma abun yafi karfinsu tunda mata ne amma haka suka dinga chacumarsu sai ga lawan Yana zuwa kofar gidan yaga Mata wasu duk anji musu rauni ransa ya baci take yanke ya kira Yansanda ya Danna kansa gidan dakin ummi yaje yaga yagwalgwal da Laila akwance har sun tauye

Idonsa ko gani bayayi wayai muku haka Laila ta sume yagwalgwal ce Bata Suma ba ita ba yawa Amma ba Baki sai kuka kanwar Babar Laila ce tace lawan dama baka fi karfin gidan kaba matarka Yar ta'addace ta kashe Laila tuni yai dakin Yana zuwa yaganta tai wiki wiki a uwar daka daya dan kota ya shaketa  tun tana ihun sai data dena ta koma tari ido ya kakkafe sai ga Yan sanda sun shigo da kyar aka bambare shi daga jikin ta tuni ankama matan Amma wasu sun tsere ido duk ya raina fata

Mom ce tace to rasa kunya  baka ga surukan naka bane ya sosa keya yi hakuri mom yanzu zan gaisa dasu ya karaso ya durkusa har kasa ya gaidasu suka amsa Masa a kunyace irin na surukai Dan Yana basu girmansu shiyasa suke kaunar sa ya karasa ya zuba mata ido duk ta rame sannu nafeesat Tai murmushi yauwa kina wahala tai murmushi shiko haushin ta yake ji Wai ciki ko amarci basu gama ci ba duka auren nasu wata nawa wata uku gaskiya da sake yai shiru Yana danne dannen  waya yai musu sallama ya fice ya tafi wajen killer dan ya rantse ranar data koma ranar ze zubar da cikin dan ba komai a ransa se Maryam yana san Maryam baze iya rayuwa ba ita ba

Daddy Yana fita park yaje inda suke hutawa da abokansa ba kowa sai amininsa alhaji sabi'u ya zauna jagwab jiki ba kwari suka gaisa Alhaji Kamal lafiya naganka haka yai shiru ba komai alhaji sabi'u a'a wallahi da komai bansaba ganinka haka ba meya faru meya same ka kagaya mun damuwar ka Ni kaina ka sani a damuwa yai murmushi ba komai ka kwantar da hankalin ka yanayine kawai ransa yai bala'in baci nizaka cewa yanayi alhaji Kamal tun muna yara muke tare nafi kowa sanin halinka a duniya

Murmushi yayi hakane aminina Ina cikin matsala wadda na rasa yazanyi da raina jarabtace Allah yai mun jarabta alhaji jarabtar me hmmmm alhaji sabi'u Allah ya jarabceni da soyayyar yarinya karama Yar cikina auren da tun da kuruciya ta ban ba sai yanzu kuma wai Yar cikina kanwar matar dana Ina cikin wani yanayi inajin zan iya mutuwa idan na rasata bansan haka so yake da zafi ba bantaba tunanin zanso wata bayan hajiya ba bantaba zato ba

Hhhhhhhh wallahi alhaji Kamal kaban dariya to shi ne me kagani kana so Allah be Haram ta maba akan me zaka haram tawa kanka Allah baya dorawa bawa abunda baze iya ba Kai kutumin kirki ne Allah baze jarrabe ka haka kawai ba akwai manufa a cikin hakan Dan haka tun yanzu kagaya wa hajiya aure zakai koda ko baka Gaya mata wazaka aura ba kabari sai nan gaba Amma ni a matsayina na amininka naba ka wannan shawarar kaso abunda ranka keso tsoho da kudi yaro Dan Haka ka saki jikin ka aminina

Hmmm banki ta taka ba kana ganin yarinyar zata yarda hhhhh yarda kai wayaki hutu kawai Kai dai Kai komai Dan Allah ka nuna Mata soyayya Dan Allah Kar Kai amfani da kudi wajen neman auren ta ka nemi yarda da soyayyar ta kaita istahara kana gayawa Allah inda alkhairi Allah ya tabbatar Amma Ni wallahi jikina nama bani da alkhairi suka kwashe da dariya ni kaina alhaji sabi'u haka nake ji inasan ta Maryam sunan ta sai Kuma mutane suka fara taruwa suka hau wata hirar suka bar waccen maganar

Dare yayi arfan ne ya dawo asibiti niki niki da Kaya ya gaida umma da mama da mom suna zaune suna hira gefe ga Maryam a zaune tana lazimi sai ga babansu nan suka gaishe shi duka nafeesat nata bacci arfan yaji dadin shigowar abban sai aka kira sallar isha suka mike suka fice masallaci tare bayan sunyi sallah sun fito arfan yake cewa Abba niko Abba alfarma nake nema banaso Maryam takwana anan kaga za'a bar gida ba kowa inaso mu koma kaga aikin dare nake sai tai kwanciyarta tayi mana girki da safe taiwa Yan asibiti ga megadi yau ko abinci be ciba a haba arfan sai ka nemi alfarma Dan wannan ai nabaka maryam

Duniya da lahira ta Zama yarka yaji dadin hakan ya karkace ya bashi rafa guda ta dubu hamsin hannunsa har rawa yake gaskiya naji dadi yadda kake kulawa damu nama alkawari ba abunda zaka nema ka rasa daga gareni Nan da sati biyu zamu koma sabon gidanmu daka bamu ba abunda zamuce ma sai godiya ba komai Abba kadena godiya suna tsaye daddy yazo suka gaisa Abba kamar ze sujjada shima daddy sai sunkuyawa yake a lallai kunya yakeji haka suka shiga dakin tare nafeesat ta farka sukai mata sannu gaba dayan su

Bayan an danyi hira sama sama daddy yace da mom ta tashi su tafi tai musu sallama tace zata turo mara me mata aiki yanzu driver ya kawo ta da abinci sai ta ta yasu kwana daddy yace arfan ya bishi ya dakko Kaya a mota ya ajiye wa su mama rafar dubu dari dari ya bawa Abba rafa biyu Amma kamar zeyi me dan kunya Abba kamar zeyi sujjada Dan murna har waje ya bisu Yana masa godiya yace baya so tafiya yai ya barsu a wajen arfan ya bishi a zabure ya dawo dakin yana baza idanuwa Ina kudin mama ta Galla Masa harara wallahi kai dai kaji kunya kaci rabon ka kaci na wani to wallahi bazamu baka ba ko kunya baka ji ni kike gayawa haka

Sai ga arfan sai ya basar ya shigo da Kaya niki niki kaji ne drinks ne ma'aikatan suka biyo shi

da shi a baya suka diddire lafiya Abba ba komai ya Kama Sosa keya to abba muma zamu wuce dare ya Fara nima tafiya zami ke kulu tashi mu tafi ke Maryam tashi ku tafi gida suje Ina alhaji cewar mama ga Yar uwarta anan ba inda zata wallahi sai taje inba Haka ba sai dai kusan inda dare yai muku ina magana kuna magana Abba barta Mana tunda basa so wallahi idan Maryam Bata bika ba a bakacin auren iyayensu da ba tare kuke ba wallahi sai ta bika ran mama ya baci ta mike nagaji da abunda kake Mana alhaji wallahi sai dai yau auren namu ya mutu nagaji shekara dama da talatin

_*To fans anan zan dakata sai naji comment dinku nayi typing dayawa Dan Allah Nima inga ruwan comment dayawa da sharhi Yasin comment yai sanyi Kuma shike ban karfin gwiywa Dan naga kuna cigiyarsa ne na daure nai muku amma Banda lafiya sosai kullum sai naje asibiti*_
[11/27, 6:29 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *💆DAN ISKAN NAMIJI💆*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Dedicated:to kainuwa fans1-12*

*Masu yimun comment da sharhi wallahi Ina sane daku insha Allah zakuga pages dinku kuyi hakuri Ina godiya da kulawarku da yadda kuke kaunar novel dina*
```

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

65-66

Wallahi auren ya mutu arfan ne ya Fara magana kiyi hakuri mama tunda bakyaso dama Dan Kar abar gidan haka ne da ga masu gadi ba abinci masu bawa shukoki ruwa duk sun Saba karbar break fast Kuma kaga basu San bata da lafiya ba tunda yau ma an basu na safe shiyasa ni bama a gidan nake kwana ba amma ba komai mama kunya ta lullubeta saboda sirikin tane shiru tayi nan Abba ya samu bakin magana wallahi sai ta bika niba tsohon banza bane

Ita ko maryam Suma ne kawai batai ba ai ba kullum ake basu abincin ba tunda Suma ba kullum suke girkin ba ran nafeesat ya gama baci ta kifa kanta a kan gado tana ta kuka umma ta mike ita kanta ranta ta baci Kai arfan dau Maryam ku tafi gida a'a umma nace ka dauketa kuje wallahi ba inda zani yar'uwata a gadon asibiti Ina ni Ina bacci wallahi ba inda zani sa'arki ce ni ina fada kina fada wallahi nazo nan sai na gwara kanki da garu jiki a sanyaye ta mike tana hawaye tuni arfan yai waje ransa kal dan dole yau ya gyagije yasha amarci da amaryar sa ya dibi dabge

Mama ce ta kalli Abba wallahi alhaji kaji kunya saboda abun kunya a gaban sirikin ka sai ka nuna halinka baka tunanin yarka mace bama zargin arfan dan yaran kirkine Amma kodan halin rayuwa nema kake kasa rayuwar Maryam a garari kaje kayi duniyace Maryam wuce kije kome ya sameki shiya ja miki da da uba yanzu tsoro akeji bare kuma mijin ya banasan haka karki Kuma yimun haka Ina magana kina magana Abba ne ya fada a fusace yayana ba lalalattu bane ban taba Zina ba yayana bazasi ba wuce karna Saba miki Kuma kiyo farfesu me kyau kinji nagaya miki

Dan nima anan zan karya ke Kuma wuce muje warar mana kayan mu ke kuma umman yara debo lemunan kisa mun a mota umma tace to mama ko harara ta zabga masa kaga ku tafi da ita danni bazan bika ba wallahi Kememe mama ta kafe sai umma ce tayi hakuri ta ta debar musu kajin da kayan fruit din ta Kai motar sannan ta dawo ta dauki lemu nan takai musu mota wuce muje nafeesat kuka take ta rungume Yar uwarta tana jin kokonto akan arfan aranta Amma ta danne haka ya tankada keyar Maryam suka fice suna fita mama tasa sakata ranta a bace ta hau gefen gadon tashi mi magana nafeesat

Ta mije zaune tana ta sharar kwalla nafeesa ban yarda da mijinki ba Sam banyar da dashi ba wane iskanci ne zesa ya hana Maryam komawa gida wace yace tazauna a gidan yayyyen ku kunsan bama so daga jiyyarki sai abu ya zama tashin hankali bakya tunanin duniya ta zagemu dagake harmu ace mun Kai Masa Yaya mun ajiye wannan wane haukane me daki shiyasan inda yake Masa yoyo ya kamata kigane takun mijinki niba yarinya bace akanme kome ya faru chaza'ai dan ba yata bace shiyasa nabar rayuwarta ta lalace wace yace tai karatu duk cikin ku wayanda mazansu keso sunyi saboda haka ki gaggawar soke wannan maganar idan lallai mijinki yanason karatu to yasaki Amma ba Maryam ba

Ina umartar ki lallai Maryam ta dawo gida gaban uwarta banasan tashin hankali Amina tana da kawaici tana girma mani bata taba sabamun tun daga sanda babanku ya auro ta to Dan Allah Maryam kiceceni banaso asamu wata matsala daga garemu idan yanaso tai karatu tayi agabansa idan nauyin ta ze dauka kotana gaban mu ze iya dauka karatu ne sai kayan aure da yai alkawari ke yarinya ita yarinya tsiran wata tara ne a tsakanin ku waze gayawa wani yaji Dan Allah ki temakeni nafeesa ki fitar Dani kunyar uwar Maryam Bata bambanta ku Dan Allah nima banasan banbanci tsakanin ku

Kuka nafeesat take wallahi Mama Abba ya hanani magana yace idan nasa bakina amaganar nan Allah ya isa bansan meyasa ba shi arfan baya shiga shirgin Maryam nafi tunanin Abba ne ya tusa masa ita akan lallai sai ya riketa bama ya yarda mi maganar hade rai yake arfan beda matsala baya kwana ma a gidan aikin dare yake idan kinga sun hadu da safe ne breakfast Amma zanyi iya kokarina nasamu ya lallaba Abba sai ta koma gida tunda hankalin ki yafi kwanciya Amma yadda zankula da kaina haka zan kula a Maryam kiyi hakuri mama ki sassauta fushin nan dan Allah

Fadan dakikai zesa arfan yayi tunanin ko kina zarginsa yayi mana ubana ne shi mara kunya sarakan San mijin masifa ana nuna muku hanya Kuna kaucewa wallahi ba'a ciwa namiji alwashi nadai Gaya Miki lallai naga Maryam ta dawo gida gabanmu shine hankalin kowa ze kwanta satin ta biyu da candy ko gama Jin dumin uwarta batai ba dan zalunci ace anra basu ita ba aure akai Mata ba Mama haka tadinga fada kamar ta ari baki har doctor ya shigo ya sawa nafeesat ruwa da allurai tai bacci ran mama a bace dakyar taci abinci tayo alwala tahau dadduma tana gayawa Allah bukatun ta tana zaune har bacci ya dauke ta tosu Mama asuba tagari

Karfe Sha biyu dot alhaji ghali suka fito daga dakin su shida baby Chakwai baby Chakwai ya dau wanka ya wani sakalo hannun alhaji ghali kamar makaho da dan jagora suka nufo parlour din banda kamshi ba abunda suke baby Chakwai yaci sarkar kafa ta gwal hannu da kafa duka gwala gwalai ne nauwara na zaune taci kwalliya a parlour abun sai wanda ya gani tayi kyau duk da farin na kantine amma tayi kyau abunta kutumar bura uba kan uban nan Kai wasu irin manyan zagi baby Chakwai ya Fara saka wanda ya firgita nauwara da shi kansa gogan alhajin uban waya baki damar kwalliya a gidan nan wallahi sai kin gayamun wanda yace ki kwalliya har ki zauna a parlour haka alhaji ghali ko sai baza ido yake baby Chakwai ya watsa Masa harara to munafiki kodai Kaine

Jikin sa har rawa yake wallahi bani bane baby na tambayeta dan ubanta tai ma bayani auho koda naji wallahi da harkai saika gane kuren ka dan bana daukan wargi bazakai mun iskanci ba nan nauwara ta mike a tsigale kai dan daudu dan iskan banza wanda Allah ya tsine musu la'ananne mijina naiwa kwalliya kuma banga uban daya isa yace akan me ba auro ni yai Dan haka kayi kadan ka hanani sararawa a gidana ransa ya baci idonsa sai ja ko gani bayayi Yana zuwa ya wanka Mata Mari ya Kara Mata yasa kafa ya kwarfeta jikake dam ta fadi dan uwarki nine dan daudu dani zaki kishi to bari in kashe ki sai ki kishin dani a kiyama

Nauwara ba baki dan ta doku tuni ta Fara kuka yadinga ball da ita yana timarta gashi namiji majiyin karfi ya ware kwanji da kyar alhaji ghali ya bashi hakuri ya hakura yana ta lallaba shi haba baby na alhaji kana jin metake fada kuwa kasan meyake cewa alhaji ni take kira Dan daudu bada ke take ba baby dani take nine dan daudun na yarda be hakura ba ya kara take ta saboda tun tana kuka tana zaginsa har tayi shiru yi hakuri baby muje ki Kara wani wankan idan

Kika sake na dawo na ganki anan wallahi sai na kashe ki ke na haramta miki fitowa indai ina kasa kuma bake ba saka wasu kaya masu kyau inaso indinga yi miki kallin villeger saboda kar Alhaji yaganki ya yaba

Da kin gama abinci to ki koma daki nagaya miki banza kazama Yar talakawa makwadai ta banda kwadayi inaake ina Alhaji Ghali wutsiyar rakumi tai nesa da kasa alhaji nawane Ni kadai ya tsirta Mata yawu suka wuce harsun tafi Alhaji Ghali ya dawo kindai ji abunda baby yace kuma wallahi kika Saba sai kin koma gidan ku dan sakin ki zan a sati na auro wata wadda ta fiki komai a duniya suka wuce daki yai wa baby Chakwai wanka ya Sanja Masa kaya ba abunda yai bare kayan jikinsa daga duka sai wanka suka kara fitowa tuni ta rarrafa ta koma dakin ta ta rufe tana kuka

Tana nadamar kwadayi irin nata daga ganin mutum ta dafe Masa ashe macuci ne suka bude cooler yawunsu sai tsinkewa yake alhaji ghali ya kwalawa nauwara Kira ta fito a firgice tana dingisawa ya banka mata wata uwar harara to uban kine ze seving dinmu ko uwarki da sauri ta karaso ta Fara  hada musu tana zubawa alhaji ghali baby Chakwai ya Kara ingije ta ta fadi ta mike tana hawaye da nadamar rayuwar ta sai me suna sa abinci abakinsu suka furzo dan ubanki mugunta zaki mun saboda bake kika siya ba Alhaji Ghali ya waska Mata wani bahagon mari dake bahago ne baby Chakwai ya daga plates din duka dana cooler ya juye Mata akanta gashi da zafinsa ta saki wani ihu ta sume a wajen

_*To fans bari indaka anan nagaji yasin masu ganin kamar Labarin nan kanar baze yiwu ba wallahi labarina true life ne nasanja wasu abubuwan ne na cire wasu na rage dan walllahi abunda akai yafi haka muni na Kara wasu Dan Labarin ya tafi Dadai  kawai fatanmu Allah ya rabamu da Dan Iskan Namiji kawai da kuma kwadayi dasan zuciya sai naji ku masoyana nice taku me kaunarku*_

*Feedyn Bash*
[12/11, 9:10 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *🧑‍🔧DAN ISKAN NAMIJI🧑‍🔧*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*~Assalamu alaikum my fans kuyi hakuri najina shiru da kukai kwana biyu hakan ya faru ne saboda rashin lafiya danake fama da ita amma alhamdulillah naji sauki yanzu na warware zaku dinga jina akai akai nagode da jumurin bibiyata da kuke masu mun magana private kuma nagode sosai da kulawa~*

*Bissimillahir rahmanir raheem*

*Second to the last page*

67-68

Banda masifa da bala'i, ba abunda baby Chakwai yake.Ko ta kan nauwara basu bi ba suka koma daki, ran baby Chakwai ya gama baci gashi yana bukatar abinci, cikin bacin rai ya daga waya ya kira yaronsa, yasa yayo musu take away yanzu ya kawo musu.Shi ko alhaji ghali yai tsiru tsiru, dan bala'in tsoron baby Chakwai yake, Baby Chakwai yai masa banza be kula shi ba, dan ransa ya gama baci, ya bude fridge din dakin ya dakko kwalbar wine dinsa, ya daga sai daya sha ta ishe shi ya dire a wajen, ya fara yiwa alhaji ghali bala'i, "akan me zaka bar nii da
```

yunwa wallahi bazan zauna dakai ba na lura wannan yarinyar sake ta samu daga wajen ka kana ma santa naga alama."

Nan alhaji Ghali ya fara rantse rantse akan, "wallahi baya santa ya, tsane ta, shi dama ba ita ya gani ba nan ya shiga kare kansa",Baby Chakwai banda masifa ba abinda yake cikin maye, Yana wannan halin bacci ya dauke shi. Alhaji Ghali ya salallaba ya fita, ya daga nauwara wadda duk ta kone, (saboda abincin da baby Chakwai ya juye mata) ya dauketa da hanzari yai dakin ta da ita, ya samu ya cire mata kayanta, yai bandaki da ita ya sata a bahon wanka, ya sakar mata shawa tai wata irin ajiyar zuciya! tana bude ido taga Alhaji Ghali.Ta fara jada baya zata sa ihu, ya rufe mata baki, "kiyiwa mutane shiru wallahi baby na yazo kin janyo mana bala'i mu dukan mu"

Tai gum banda radadi ba abunda jikinta ke Mata, dan har wuyanta ta konu sosai daurewa kawai take, Allah ya temake ta kadan ne ta tashi kunar, yai mata wanka ya fito da ita ya zaunar da ita akan gado, ya kalleta ya sheke da dariya! "nauwara ko? karki ga nai miki haka ki dauka sanki nake, wallahi ban taba sanki ba dan kema nasan ba sona kike ba, dukiya ta kikewa ga dukiyar nan inzata ciyu ki cita.Abunda yasa kika ga na temake ki banso ki nakasa na rasa yar aiki a gidana, ya kad'a kai yai ficewar sa.

Ihu ta saka, "yau na shiga uku! ina zansa kaina, dama ya gama ganoni, innalillahi wa'innailaihirraji'un", ta dinga kuka tana salati, saboda azabar zugin da radadin da kafadar ta ke mata, banda kuka ba abunda takeyi, cike da tausayin kanta da rayuwar ta a wannan bakin gidan,( sunan data  sawa gidan kenan) nan da nan zazzabi yai mata sallama, tana ta karkarwa jikin ta duk ya saki, taji ana ta nocking amma shiru ba wanda ya leko, haka ta sadada da jan jiki tayi parlour, ta murda key din ta bude kofar.

Yaron Baby Chakwai ne ya kawo musu abinci. sai me idonsa ya sauka akan Nauwara  jiyai wata muguwar sha'awarta na fusgarsa, dan best ce karama a jikin ta, ya kare mata kallo ya ganta a jigace take. "beb ina masu gidan", tai rau da idonta,"bacci suke" ok, "na kawowa anty Chakwai abinci ne, kimin magana da ita." gabanta ne yai wata muguwar faduwa, "ni kuma" bata san sanda ra furta ba, "eh ke koba me aiki bace" a'a "matar gidan ce" what? ya fada da karfi,

anty da kishiya, chab akwai matsala, nan ya lallatsa waya ya kira, sai da ta gaji da ringing sannan ya daga, har yanzu dai mayen be sake shi ba, "ya akai habu" "anty gashi na kawo miki abincin," Ok gani nan minti goma sha biyar.

Nauwara ko ta tafi tunani, wai anty Allah ya halicci mutum a namiji ya koma mace, mutane ko kunya basaji, "muje ko koba zaki iya mikewa bane sai in daga ki", ya fada cike da salon yaudara, yana wani kanne mata ido, mikewa tai ta fara bin bango, nan ya hango yadda ta kone, kai lafiya? ya karasa kusa da ita ,ya shiga dubawa, nan ta fashe da kuka, dama ba karamar azaba take sha ba, "konewa nai" ya salam "amma baki je asibiti ba, shirya na kai ki".Gabanta yai muguwar faduwa, dan tasan dokar ta a gidan, "baze barni ba", wake nan ?"Baby Chakwai" hhhhhhhh ya sheke da dariya dama anty ce ta auro ki? ikon Allah! "ashe ta fara zama namijin ta, da har ina tunanin nima indan dibi garar ki, ashe kayan manya ne na dauka matar alhaji ghali ce."

"Ba shi bane mijina, Alhaji Ghali shine mijina". Ido ya zaro, "ke baki da hankaline?  ina ke ina kishi da anty Chakwai, kiyi maza maza kisan nayi, maza ma basa iyawa bare ke, sai yasa a salwantar miki da rayuwa, yana da mugun kishi," nan ya shiga bata labarin ta'addanci irin na Baby Chakwai.Hankalin ta ya kara tashi, katemaka mun nabar gidan nan dan Allah, nayi nadamar auren alhaji a rayuwata, "baki yi nadama ba tukun sai kinga anfita da gawar ki daga gidan nan, sannan zaki shiga hankalin ki dani." (cewar Baby Chakwaiya da yake fitowa) ya galla musu harara, kai habu meya hadaka da wannan karfar? jikin sa na rawa anty wai cewa tai na temake ta na kaita asibiti, shine take cewa tayi nadamar hada kishi dake.Hmmm! "barta habu bata da mutunci, tabar ni da yunwa dan iskanci,ba abinda ta iya wallahi sai na dau mummunan mataki akanta."

A'a anty, meze hana idan bata iya ba nazauna daku na dinga koya mata,  koya kika gani? hmmm! "hakan ma yayi," "yauwa anty ina godiya, alfarma nake nema abarta taje asibiti, "baze yiwu ba habu" ya fada cikin tsawa, nan habu ya farai masa kirari kansa na kumbura, ya daga masa hannu, naji amma sai dai ka kira likitan ya duba ta a gida.Nan da nan ya kira likita, minti talatin yazo yai kata dressing din wajen, tasha kuka da ihu harda majina, ya bata magunguna ya tafi  Alhaji Ghali da Baby Chakwai na gefe, banda dariya ba abunda suke babbaka wa, sunci sunyi dam, sai ga masu decoration da masu make up sunzo.

Hankali kwance a ka fara kawata harabar, dan sunsan ba ruwansu dasa ido, masu decoration din ma daga dubai suke, haka masu make up, karfe uku aka fara taruwa a bakin gate yan budar kai, sai me suka tarar da sojoji a bakin gate, sukai sukai suka ce sam ba'a basu izinin kowa ya shiga gidan ba. Da suka damesu suka dakko bulalai, nan aka zuba yar tsere, suka watse kowa na tofa albarkacin bakinsa, nan wasu sukai gidansu amarya dan kai rahoto, karfe biyar gida ya fara cika da tantiran maza, wayanda suka riki duniya, wayanda suka sanja halittun da ubangiji yai musu.

Anzagaye kowane table da kalolin abincin, yan china su aka dakko sukai girkin, manyan maza ne masu ji da kudi, wayanda suka shahara sukai suna a duniya, sune a wajen gidane, mahaukacin gidane, kowa da inda ze ajiye motarsa ba tare da kowa ya dami kowa ba, karfe shida aka fito da amarya da ango, wanda sun gaji da haduwa iya hangen ka bazaka taba cewa Baby Chakwai ba mace bace, nan aka fara tafi da murna banda kida ba abunda ke tashi, ga wani uban durmemen cake a gefe da zasu yanka, shi kansa abun kallo ne, nan aka fara taro wuri ya hautsine kowa da beb dinsa, manyan maza masu ji da kudi da iyalansu da komai, amma gasu anan suna lalacewa.

Baby Chakwai ya gama duk wani plan dazeyi yasa akashe Nauwara. Dan yayi rantsuwa baze zauna da kishiya ba,maza ba amana ze iya zagewa ya dinga nemanta, bukata ta biya tunda duniya ta sheda cewar Alhaji Ghali yayi aure, saboda haka yasa abatar da gawar yadda ba wanda ze san cewar ta mutu, ya hana nauwara fita ko ina ya kulleta a daki, yasa key yana fitowa ya bawa wanda yasa ya kasheta key din. (su kuma suna chan, anata budiri anata zubar da nera, anata badala wadda bazata faduba, kazanta ce me tsananin datti, sai dai fatan Allah ya tsaremu, ya karemu ya kare mazajen mu, da yan uwanmu da 'ya'ya yenmu, ka tsare imanin mu da dukkan musulmi ameen ya allah.)

Kannen umman Maimunatu sunzo, sun mata nasiha me ratsa jiki akan zaman aure. anty Ummi ce ta fara magana, "maimuna kibi mijinki kizauna lafiya, ke dashi duka marayu ne Allah shine gatan mara gata, allah ya gatance miki maimuna, kibi mijinki kiyi hakuri, samu da rashi na Allah ne kinyi biyayya insha Allah bazaki tabe ba, zakiga ribar hakurin ki, zaman aure yanzu dan hakuri ne, wallahi maza wahala suke dan idan ana siyan miji wallahi wasu da dama za'a siya musu.Kar kiga kin samu ki wulakanta, wallahi Allah baze barki ba, zaki nadama da danasani

duk ranar daya auro me masa biyayya, ki rike mijinki da yan uwansa da kowa nashi".

"Duk wani abu nashi ki dinga kula dashi, nasan dai ke ba baya ba wajen tsafta, a kara tsafta musamman hammata, matse matsi, da cibiya. Duk wata kafa lungu da sako a dinga kula, maza basa san kazanta, kidinga kokari wajen tsafta, shaving akai akai, kitso da kunshi, ki nemi chukwi da dabino da zuma da nono me kyau da gumba da kayan daka ki samu ki hade ki damesu, ki dake chukwi da dabino duk ki hade, kisha ki koshi wallahi maimuna zaki dade da ni'imarki, bake ba neman wani magani, ki nemi man ayu da na damo original din zaki ga baya bacci, ki hadi ki dinga insert, ki gwada zaki ban labari yata, na haneki da cushe cushe dan zaki kashe gaban ki a banza a wofi".

"Maimuna bari in barki haka, dan nasan suma kawayenki sun karu yamma tayi zamu tafi gida yau mubar umma itama ta huta, maimuna ki rike ruwan zafi, amma karki saka gishiri saboda yana kashe gaban mace, shima ruwan me dumi bame zafi ba dalan dalan , ayi hakuri azauna lafiya, sai ihu yammatan nan, "gaskiya anty mun karu mungode sosai, muma in lokacin mu yazo mun huta,zamu zo ki mana tamu lakcar," hhhhhh! "danma ba lokaci"  suka fito gaba daya sukai wa inna sallama, suka fice maimuna ta dawo ta fara gyara gidan, tai wanka tana jiran isa matukar ta ya dawo.

*To fans bari indaka anan sai naji comment dinku more comment more typing*

*Feedyn Bash*

[12/13, 7:29 PM] 👯Feedy Bash On Top💃💃: *💆‍♂️DAN ISKAN NAMIJI💆‍♂️*

*NA*

*FAREEDA ABDULLAHI*

*_🌈KAINUWA WRITERS✍🏼 ASSOCIATION_*🤝🏻
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```

https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*Alhamdulillah! Allah ya kawo mu karshen book 1, yadda muka fara lafiya mungama lafiya. Allah yasa mu fara book 2 din lafiya, mukai karshen sa lafiya. My fans, masu mun comment da masoyana, wayanda nasani da wayanda bansani ba, nagode sosai da kauna, Allah ya barmu tare Feedyn Bash ce.*

*TALLA   TALLA   TALLA*

*AKWAI SABON NOVEL DINA DAZAN FARA ME SUNA (MATAN AURE,ZAWARA,KO Y'AMMATA?) INSHA ALLAH ON MONDAY ZAN FARA BADA FREE PAGE GAME BUKATA ZE TUNTUBE NI TA WANNAN NUMBER DIN 08106795647 NAIRA 200 NE KACAL*

🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚

69-70

Yan budar kai ne I suka shiga gidan Haule. Wasu na haki suka zuzzube a tsakar gida hankalin su a tashe, ragowar wayan da sukai ragowa masu shirin zuwa suma suka firfito, "lafiya jama'a" "ina fa lafiya munga abunda ya ishe mu yau, da bindigu da bulalai aka biyo mu, daga zuwa budar kai."  Haule na daki ta saki wani uban ashar, "ubanwa ya hana ku shiga" nan suka labarta mata komai. Sai ga meena ta shigo a fujajan, dan ita data takura musu na jaki taci, sai zare ido kawai take dan ta jibgu. Hankalin su ya gama tashi, nan haule tace sai an kaita gidan, meenat ce tai karfin halin gaya musu basa kasar
```

Ta sanar da ita wayar da sukai da safe, ta shiga labarta musu, "tabbas naji tashin kida, kuma naga manyan motoci na shiga gidan". Nan kowa ya shiga tofa albarkacin bakinsa, kowa da abunda yake fada suka cika gida. Malam ya shigo haule tasa kuka wai antozarta ta, nan yai mata ta tas ya fito ya fatatta ki mutanen da suka cika masa gida, ya dinga fada, "kun gama bikin ku kunyi bidi'arku, kun kai yarinya ba wanda zezo yai mun wata bidi'a," yai ficewarsa ya bar haile da bala'i ba kafa.

Anje police station, inda aka garkame matan da aka kama, su kuma akai asibiti dasu, allah yaso fuskar Laila bata tauye ba, ga kakarta da kafa ta tauye. Ummi tafita daga hayyacin ta, akai emergency dasu saboda da yan sanda basu samu wata matsala ba, anyi musu treatment dukansu. Ummi ta farfado ta warware an sallameta, inda take lawan ya yanka mata visar zaman gida, ya bata jan kati yai mata saki daya, nan ta dinga zundum ihu tana kuka. 'Yan sanda sukai mata raraf suka kara gaba da ita. Aka kirawo iyayen ta, dan wayanda tasa aikin da sukaci jibga sunce biyansu tai, akan su nakasa kowa da kowa inta kama a kashe Laila.

Idan kaga Ummi a cell ita da mukarraban ta dole ka tausaya musu, dan sun wahala dan lawan chayai suma ai musu lilis suji a jikin su. Kowacce sai da aka kirawo mijinta, inda wasu mazan take yanke suka ce su wuce gidan su, wasu ko da takardar su a hannu. Ummi tasha tsinuwa da tofin alatsine, babban abun haushin naira dari biyar biyar ta basu, abunda ya fusata mazajen su kenan, manyan wayanda suka tunzurata zawarawa ne. Sun kaita sun baro, iyayen ta ne suka zo sunyi fushi me tsanani da ita, inda aka bada belinsu amma da sharadin idan suka kara aikata irin wannan sai sunyi prison. Yanzun ma dan kawun Laila yace ya yafe ajanye bayaso, shiyasa amma lawan beso haka ba yaso akai su prison suci gabza.

Alhamdulillah jikin Laila da Inna yayi kyau, masha allah satin su uku aka sallame su,  direct gidan ta aka maidata. Inna ta wuce gidan kawu saboda jikin girma, Hankali kwance Lawan da Laila suka ci amarcin su, sai dai ba ganin mutuncin juna, saboda duk albarkar auren sun zubar a titi, satin su biyu suka fara bala'i, saboda lawan duk wani abu dayake ba abunda ya ragu sai daduwa, barikin sa yake bugawa. Laila da kishi kullum sai anyi bala'i andaku, ta saki jiki ya sallami Ummi anata haukan ta mallake shi ita kadai, bata san cewa sam ba haka a ransa ba, dan yanzu anyi nisa da shirye shiryen auren su da Doctor Saudat, amma a boye dan baya san kowa ya sani, ita kuma ta bishi a haka, gefe guda tai alkawarin daukan fansar abunda yai mata a asibiti.

Dan tai rantsuwa akan sai ta dau fansar keta mata mutunci dayai, sai ta sa shi nadama da dana sani a rayuwar sa. Shiri suke sosai na auren. Lawan sai zakwadi yake da rawar kai, burinsa ya aure ta riba biyu ga kudi ga gida, hankalin sa kwance tunda hajiya santalos bata dawo ba tana saudi, tace sai nan da shekara daya akwai abunda ta tsaya yi. Amma  ta sanar masa lallai idan ta dawo ba fashi, satin za'a daura musu aure. Shiyasa ya saki jikinsa yake abunda ransa yake so, burin sa ya mamaye mata dukiya ya sallameta, yanzu takan doctor ze fara. (maji magani idan burin Lawan ze cika akan doctor, ko kuma burin Doctor ze cika akan lawan)

"Ke yanzu ko kunya bakya ji?dubeki godai godai dake a gida,wallahi nagaji da cida karti a gida,keda yayanki,wallahi tun wuri kusan abunyi."Ummi ce ta fashe da kuka,"haba umma yanzu kema bazaki tausayamun ba, dame zanji tunda na taho Lawan be kara tunani ba, kona kirasa baya dagawa,yabarni da yaransa. Dan Allah umma ki temaka mun, ku kira shi na koma dakina"Ummi "baki da hankali ne? to maza kicire lawan aranki ke ko kishin zuci baki da shi,to ko maza sun kare kinbar auren dan iskan chan.

Wani gululun bakin ciki ne ya tokarewa Ummi. Umma inasan sa kuma komai lalacewarsa shine uban yayana,kuma ba lalacewa a aure Umma, na tabbatar ibada nake, kuma kullum ina masa addu'a Allah ze shirya shi"."To uwar iya tsara zance kinsan da haka kika ki zaman auren? kika dawo gida, to sai ki dau harama ki fara shiri, dan awara zaki fara siyarwa da safe, da daddare kidinga wainar fulawa, madinga ragewa tunda kinsan shi kansa malam yana bukatar temako, nagaji da cida kartin banza." kuka Ummi ta rushe dashi, "kyayi kya gama ke kadai", tabar Ummi a wajen tana ta kuka.

Zuciyar ta na suya da radadi, ta cika da tsanar laila, tana mamakin butulci irin na maza, duk dan saboda shi tayi amma ki duba irin sakamakon abunda yai mata. Gashi ko ta fita ba dadi kawayen ta sun gujeta, kowa haushin ta yake ji, saboda ita wasu sun rasa auren su, shiyasa sam bata jin dadin zaman gidan.Ga gorin umma na safe daban na dare daban, har wani suna ta sa mata me bakar kafa, tarasa ina zatasa kanta,haka tayi kukanta ta gaji, tayanke shawarar zuwa gun aikin lawan ta same shi,bata tsaya bata lokaci ba tai wata fitinanniyar shiga, da tasan dole ta rikita Lawan dan tasan halin gogan nata.

Tana zuwa company din ta nufi office dinsu,dama tasani kuma mutanen wajen sun santa, bata sha wahala ba tasame shi,yasha kayarsa yayi tatil yayi dif dashi yana zaune shi kadai, abokin aikinsa baya nan ya dago da runannun idanuwan sa,gaba daya ta gama tafiya da imaninsa, wata ajiyar zuciya ya saki hmmmmm!be wata wata ba ya dannawa kofar sakata, ta riga tasan meyake nufi ta saki wani murmushi,amma kasan yanzu niba matarka bace ko?dole sai ka maidani sannan komai kammala," ba bata lokaci yace, "namaida ki bani kayana dana kwana biyu ban hau ba", tai murmushi "mu hadu a gida" ta zura da gudu ta zare sakata tabar shi da cizon yatsa. Ya dinga tsine mata albarka, gashi yau Laika bata zoba bata da lafiya, itace kuka me dadin hawa, yana zuwa zeyi ya wuce.

Bakin ciki ya ishe shi, kawai ya rufe kofa ya kama bango yadinga buga masa gwatso abunsa, ko zafi bayaji sai daya kai geji sannan ya hakura, ya bata bangon yai kacha kacha be damuba yai ficewar sa yabar office din. Sabon gari gidan karuwai na premier yaiwa tsinke, yasamu wadda yakeso ya shige dakinta, dan yai zuciya ta janyowa Laila ma baze kwan a gidan ba kowa ya rasa. Ummi na komawa ta hau hada kayan ta, ta hada kan yaranta,tace "to umma mu zamu wuce" umma ta zaro ido, ina tai murmushi "lawan ya maidani dakina", "baki isaba ba inda zaki" "ta isa ko zoki wuce allah ya kiyaye hanya." cewar babanta cike da murna suka fice.

Arfan suna tafiya kala ba wanda yace tsakanin su,haka suke ta tafiya, maryam na share kwalla cike da tausayin rayuwar su ita da yayar ta. Ta rasa wane irin uba Allah ya basu, wanda sam besan ciwon su ba. Arfan be zame ko ina ba sai yahuza suya, ya siya musu kaji dasu ice cream yayi musu siyayya sosai, bata ce masa kala ba. "Maryam me kikeso mezaki ci?" banza tai masa, yagaji da surutun sa yaja motar suka wuce gida. Yana parking ta bude motar tai cikin gida, a fusace dakin ta ta shiga ta danna sakata, ta bude pridge din dakin ta dakko lemon nata, exotic me mugun sanyi ta daddaka san ranta.

Ta cire kayan jikin ta ta dan kwanta, daga ita sai bra da bon shot, minti biyar maganin ya fara aiki, ta fara fita hayyacin ta. Arfan na shigowa yaga ta rufe kofar, murmushi yayi ya wuce sama, yai wanka ya sanja kayan sa yasa gajeran wando kawai, ya sakko da kansa ya shiga kitchen, ya dakko plate ya juye kazar, ya dakko plates ya yanka musu fruit akai, ya dakko mata exotic shi kuma ya dakko fresh milk, ya dauki extra key ya bude dakin. Tai dai dai a gado tana ta hawaye, tana ta juyi ta rasa yaza tayi taji an bude kofa, a firgice ta mike taga arfan ne, jikin ta

yai mugun sanyi, duk wannan tsanar da take masa jitai ta kau, bata da burin daya fi taji ta a jikin sa.

Ya fuskanci ita kanta a bukace take da shi. Murmushi yayi "maryam nasan kema kina bukata ta, tabbas kema kin kamu soyayya ta, be kamata ki guje ni ba masoyiya." Ya dinga mata maganganu da yaudara, a hankali ya dinga matsawa jikin ta, ya samu ta yarda dashi sai da suka fara ci suka koshi, sannan suka fada duniyar masha'a. Duk da haka kuka tadinga yi masa, har yanzu ta kasa sabawa zafi take ji, a haka ya din ga bi da ita yana sarrafa ta, yana kukan dadi tana kukan azaba, haka har ya gaji ya kyale ta. Nan ya fara sambatu "maryam bazan iya rayuwa bake ba, ki amince dani dan Allah, kiban shawara yaza'ai na mallake ki.

Momy ce ta kalli daddy, alhaji lafiya kuwa meye matsalar ka, gaba dayan ka naga ka zama wani sukuku lafiya? murmushi! yayi "hajiya kenan uwargida ran gida, akwai magana, amma inaso kimun kyakyawan fahimta, idan munje gida zan sanar dake komai, amma dan Allah ki kwantar da hankalin ki kinji tawan." Haka kawai taji gaban ta na faduwa, kasa magana tayi har suka isa gida. Daddy yai parking suka wuce cikin gida, ma'aikata nai musu sannu da zuwa suka wuce sama. Jitai bata da kuzari ko yar aikin bata aikawa su Nafeesat ba, ta hau sama daddy na lure da ita, "haba hajiya gaskiyana fasa gaya miki, tun ba kiji ko meye ba kin daga hankalin ki" tai murmushin karfin hali, dan kirjin ta banda bugawa ba abunda yake, "wallahi ba komai alhaji tausayin yarinyar nan ne kawai" bayan sunyi wanka dukan su suka ci abinci suka koma sama.

Alhaji ne yai gyaran murya, mommy ta gyara gyara zama, yai shiru sannan ya fara magana. "hajiya ina so kimin kyakyawar fahimta, ki fuskance ni ki gane cewa komai nufi ne na Allah, bawa baya kaucewa kaddarar sa, hajiya abunda kika dade kina cewa nayi ne na kasa, yau Allah ya jarabce ni da shi. Hajiya soyayya ce ta kamani ta yarinya karama yar cikina. Kuma auren ta nakeso nayi ba da dadewa ba, bazan aure ta dan na bata miki ba, ko cusguna miki, zan aure ta ne dan raya sunna." Kirjin momy ya shiga bugawa amma ta dake, a ranta kawai maimaita kalmar aure take.

Hmmm! "Naji Alhaji wacece yarinyar? kuma a ina take?" tambayar tazo masa a bazata. Yai dana sanin gaya mata maganar, "magana nake a ina take." Sai da yaja dogon numfashi yai huci

ya fesar, umm....umm dama ba wata bace ba bakuwa bace, yarki ce ma, yata kuma Alhaji yata daga ina
? daga wane bangare? tayaya ma zaka auro mun yata?" ta kafe shi da idanuwa, "ina jinka" "maryam ce kanwar Nafeesat" wata zabura Mom tai. "Me kace banji ba wace maryam din bangane taba?"shi ma yai fuska, "maryam kanwar matar arfan" what? ta fada da karfi "innalillahi wa'inna'ilaihir raji'un" abunda ta fada kenan, ji kake yifa ta fadi ba numfashi a tare da ita. Da gudu daddy yayo kanta dif ba numfashi, ya bude pridge a gigice ya zuba mata ruwan sanyi amma shiru, ihu shi ma ya kurma.

🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚

*To fans nan na kawo karshen Dan iskan namiji book1. Sai mun hadu a book 2 insha allah, akwai sabon novel daban fara na kudi, me bukata ta tuntubeni ta wannan Number 08106795647. Naira 200 ne kacal, zaka turo da kati ta wannan Number, ko Account Number, 0019681503 stanbic ibtc bank, Fareeda Abdullahi Ibrahim, sai na jiku fans.*

*Nice taku a kullum, a koda yaushe.*

*Feedyn Bash* *Feedyn bash*